الجزء ١٠ الحزب ١٩

۞ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّمَا غَنِمۡتُم مِّن شَيۡءٖ فَأَنَّ لِلَّهِ خُمُسَهُۥ وَلِلرَّسُولِ
وَلِذِي ٱلۡقُرۡبَىٰ وَٱلۡيَتَٰمَىٰ وَٱلۡمَسَٰكِينِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِ إِن
كُنتُمۡ ءَامَنتُم بِٱللَّهِ وَمَآ أَنزَلۡنَا عَلَىٰ عَبۡدِنَا يَوۡمَ ٱلۡفُرۡقَانِ
يَوۡمَ ٱلۡتَقَى ٱلۡجَمۡعَانِۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٤١ إِذۡ
أَنتُم بِٱلۡعُدۡوَةِ ٱلدُّنۡيَا وَهُم بِٱلۡعُدۡوَةِ ٱلۡقُصۡوَىٰ وَٱلرَّكۡبُ
أَسۡفَلَ مِنكُمۡۚ وَلَوۡ تَوَاعَدتُّمۡ لَٱخۡتَلَفۡتُمۡ فِي ٱلۡمِيعَٰدِ
وَلَٰكِن لِّيَقۡضِيَ ٱللَّهُ أَمۡرٗا كَانَ مَفۡعُولٗا لِّيَهۡلِكَ مَنۡ
هَلَكَ عَنۢ بَيِّنَةٖ وَيَحۡيَىٰ مَنۡ حَيَّ عَنۢ بَيِّنَةٖۗ وَإِنَّ ٱللَّهَ
لَسَمِيعٌ عَلِيمٌ ٤٢ إِذۡ يُرِيكَهُمُ ٱللَّهُ فِي مَنَامِكَ قَلِيلٗاۖ
وَلَوۡ أَرَىٰكَهُمۡ كَثِيرٗا لَّفَشِلۡتُمۡ وَلَتَنَٰزَعۡتُمۡ فِي ٱلۡأَمۡرِ
وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ سَلَّمَۚ إِنَّهُۥ عَلِيمُۢ بِذَاتِ ٱلصُّدُورِ ٤٣ وَإِذۡ
يُرِيكُمُوهُمۡ إِذِ ٱلۡتَقَيۡتُمۡ فِيٓ أَعۡيُنِكُمۡ قَلِيلٗا وَيُقَلِّلُكُمۡ
فِيٓ أَعۡيُنِهِمۡ لِيَقۡضِيَ ٱللَّهُ أَمۡرٗا كَانَ مَفۡعُولٗاۗ وَإِلَى ٱللَّهِ
تُرۡجَعُ ٱلۡأُمُورُ ٤٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِذَا لَقِيتُمۡ فِئَةٗ
فَٱثۡبُتُواْ وَٱذۡكُرُواْ ٱللَّهَ كَثِيرٗا لَّعَلَّكُمۡ تُفۡلِحُونَ ٤٥



**(41) Ya ku muminai ku sani abin da kuka samu daga kafirai da qarfi a wajen jihadi a kan tafarkin Allah (wato ganima), to za a raba shi gida biyar, kashi huxu daga cikin biyar za a raba wa mujahidai, na biyar da ya rage kuma za a raba shi gida biyar: rabo xaya na Allah da Manzonsa, za a sarrafa shi a al'amuran musulmai gaba xaya, rabo na biyu ga makusanta Annabi (S.A.W) daga cikin Bani-Hashim da Bani-Muxxalib, kashi na uku ga marayu, na huxu ga talakawa da miskinai, na biyar ga matafiya waxanda guzurinsu ya yanke, (wannan shi ne hukunci) idan kun yi imani da Allah, da abin da muka saukar ga bawanmu Muhammad (S.A.W) a ranar Badar, ranar da Allah ya rarrabe tsakanin gaskiya da qarya, yayin da Allah ya ba su nasara a kan maqiyansu. Allah da ya taimake ku mai iko ne a kan dukkan komai.**

**(42) Ku tuna lokacin da kuka kasance a vangaren qasa daga cikin kwarin da yake kusa da Madinah, Mushirikai suna xaya vangaren mai nisa, inda yake vangaren Makkah, ayarin suna wani wuri qasa da ku, kusa da gefen kogin maliya (Red Sea). Da kun yi alqawari ku da mushirikai a kan ku haxu, da sashenku ya savawa sashe, sai dai Allah (S.W.T) ya haxa tsakaninku a Badar ba tare da alqawari ba, saboda wani lamari da yake tsare ya kasance, shi ne cin nasarar muminai, da qasqantar da kafirai, da xaukaka addininsa, da qasqantar da shirka, don wanda zai mutu daga cikinsu ya mutu bayan hujja ta tsaya a gare shi, ta hanyar nasarar muminai a kansu, duk da qarancin adadi da tanadinsu, wanda kuma zai rayu, ya rayu a kan hujjar da Allah ya bayyana masa ita, ba wani wanda zai zama yana da hujja a wurin Allah da zai kafa hujja da ita. Allah yana jin maganganun kowa da kowa, Masanin ayyukansu ne, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai saka musu a kansu.**

**(43) Ka tuna – Ya kai wannan Manzo – ni'imar da Allah ya yi maka, kai da muminai a yayin da Allah ya nuna maka mushirikai a barcinka yan kaxan, har ka sanar da muminai hakan, suka yi wa juna busharar alheri da hakan, azamar su ta qarfafa a kan gamuwa da maqiyansu da yaqarsu, da Allah (S.W.T) ya nuna maka mushirikai a barcinka su da yawa, da azamar sahabbanka ta yi rauni, sun ji tsoron yaqi, sai dai Allah ya kuvutar da hakan, ya kare su daga kasawa, ya qanqanta su a idon Manzonsa (S.A.W), saboda shi Masanin abin da zukata suka qunsa ne, da abin da suka voye.**

**(44) Yaku muminai ku tuna yayin da Allah ya nuna muku mushirikai 'yan kaxan, lokacin da kuka gamu, sai hakan ya baku qarfin halin yaqarsu. Ya kuma qanqanta ku a idanuwansu, sai suka gabato don yaqar ku, basa tunanin komawa, saboda Allah ya hukunta wani lamari da ya zama tsararre, shi ne na xaukar fansa a kan mushirikai da kisa da kamu, da kuma yin ni'ima ga muminai ta hanyar cin nasara a kan maqiya. Ga Allah kaxai makomar al'amura take, ya saka wa wanda ya munana a kan munanawarsa, ya saka wa mai kyautatawa a kan kyautatawarsa.**

**(45) Ya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi Manzonsa, idan kun yi gaba-da-gaba da jama'ar kafirai, to ku tabbata a yayin haxuwa kada ku ji tsoro. Ku ambaci Allah da yawa, ku roqe shi, shi ne mai iko a baku nasara, ko ya baku abin da kuke nama, ya tseratar da ku daga abin da kuke tsoro.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Dukkan ganima ta Allah ce, ya sanya ta inda ya ga dama, a yadda yake so, ba wanda yake da ta cewa a kan haka.**

**2 - Yana daga sababin cin nasara tsarin da Allah ya yi wa muminai, daga abin da zai taimake su wajen samun nasara, na haquri da tabbata, da yawaita ambaton Allah.**

**3 - Hukuncin Allah zartacce ne, hikimarsa mai girma ce, kuma alheri ce ga bayin Allah, al'umma gaba xaya.**

وَأَطِيعُواْ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ وَلَا تَنَٰزَعُواْ فَتَفۡشَلُواْ وَتَذۡهَبَ
رِيحُكُمۡۖ وَٱصۡبِرُوٓاْۚ إِنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٤٦ وَلَا تَكُونُواْ
كَٱلَّذِينَ خَرَجُواْ مِن دِيَٰرِهِم بَطَرٗا وَرِئَآءَ ٱلنَّاسِ وَيَصُدُّونَ
عَن سَبِيلِ ٱللَّهِۚ وَٱللَّهُ بِمَا يَعۡمَلُونَ مُحِيطٞ ٤٧ وَإِذۡ زَيَّنَ
لَهُمُ ٱلشَّيۡطَٰنُ أَعۡمَٰلَهُمۡ وَقَالَ لَا غَالِبَ لَكُمُ ٱلۡيَوۡمَ مِنَ
ٱلنَّاسِ وَإِنِّي جَارٞ لَّكُمۡۖ فَلَمَّا تَرَآءَتِ ٱلۡفِئَتَانِ نَكَصَ
عَلَىٰ عَقِبَيۡهِ وَقَالَ إِنِّي بَرِيٓءٞ مِّنكُمۡ إِنِّيٓ أَرَىٰ مَا لَا
تَرَوۡنَ إِنِّيٓ أَخَافُ ٱللَّهَۚ وَٱللَّهُ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٤٨ إِذۡ يَقُولُ
ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلَّذِينَ فِي قُلُوبِهِم مَّرَضٌ غَرَّ هَٰٓؤُلَآءِ دِينُهُمۡۗ
وَمَن يَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ فَإِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٤٩ وَلَوۡ
تَرَىٰٓ إِذۡ يَتَوَفَّى ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلۡمَلَٰٓئِكَةُ يَضۡرِبُونَ
وُجُوهَهُمۡ وَأَدۡبَٰرَهُمۡ وَذُوقُواْ عَذَابَ ٱلۡحَرِيقِ ٥٠ ذَٰلِكَ
بِمَا قَدَّمَتۡ أَيۡدِيكُمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ لَيۡسَ بِظَلَّٰمٖ لِّلۡعَبِيدِ ٥١
كَدَأۡبِ ءَالِ فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَفَرُواْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ
فَأَخَذَهُمُ ٱللَّهُ بِذُنُوبِهِمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ قَوِيّٞ شَدِيدُ ٱلۡعِقَابِ ٥٢



**(46) Ku lazimci biyayya ga Allah da biyayya ga Manzonsa a cikin maganganunku da ayyukanku, a dukkan yanayin da kuke ciki, kada ku sava a ra'ayi, saboda savani sababi ne na rauninku da tsoronku, da tafiyar qarfinku. Ku yi haquri yayin haxuwa da maqiyinku, haqiqa Allah yana tare da masu haquri, ta hanyar nasara da qarfafawa da taimako, duk wanda Allah yake tare da shi, to ba makawa shi ne mai rinjaye da nasara.**

**(47) Kada ku kasance kamar mushirikai waxanda suka fito daga Makkah cikin girman kai da nunawa mutane (Su sun isa) suna kange mutane daga addinin Allah, suna hana su shiga cikinsa. Allah yana kewaye da abin da suke aikatawa, babu abin da yake vuya gare shi, daga ayyukansu, kuma zai saka musu a kansu.**

**(48) Ya ku muminai ku tuna ni'imar Allah a kanku, ta yadda Shaixan ya kyautata wa mushirikai ayyukansu, ya qarfafa su a kan gamuwa da musulmai da yaqarsu, ya ce da su: "Yau babu mai rinjaye a kanku, kuma ni zan taimake ku, in tseratar da ku daga maqiyanku". Yayin da jama'ar biyu suka gamu: jama'ar muminai, a tare da su da Mala'iku suna taimakonsu, da jama'ar mushirikai, a tare da Shaixan wanda ya tavar da su. Yayin da suka haxu sai Shaixan ya juya da gudu, ya cewa mushirikai: "Haqiqa ni na barranta daga gare ku, tabbas ni ina ganin Mala'ikun da suka zo don taimakon muminai, don haka ni ina tsoron Allah ya halakar da ni, Allah mai tsananin uquba ne, ba wanda yake da ikon xaukan uqubarsa". (49) Ku tuna yayin da munafukai da masu raunin imani suka ce: "Waxannan musulmi addininsu ya yaudare su, da yake musu alqawarin nasara a kan maqiyansu, duk da qarancin adadinsu da raunin tanadinsu, da yawan maqiyansu da qarfin tanadinsu". Waxannan ba su gane cewa duk wanda ya dogara da Allah shi kaxai, ya amince da abin da ya yi alqawari da shi na nasara, to haqiqa Allah mai taimakonsa ne, ba zai tavar da shi ba, kowane irin rauni yake da shi kuwa. Allah Mabuwayi ne, babu mai rinjayarsa, mai hikima ne a cikin abin da ya qaddara, kuma ya tsara. (50) Ya kai wannan Manzo da zaka ga waxanda suka kafirtce wa Allah da Manzanninsa yayin da Mala'iku suke karvar rayukansu, suna fizgarsu, suna dukansu a fuskokinsu idan sun fuskanto su, suna dukan bayansu idan sun juya a guje. Mala'ikun suna ce musu: "Ya ku kafirai ku xanxani azaba mai quna". Da zaka ga haka – ya kai wannan Manzo – da ka ga al'amari mai girma. (51) Wannan azabar mai raxaxi yayin da za a karvi rayukan – waxannan kafirai – da azaba mai quna a cikin qaburburansu da kuma a lahira, dalilinta shi ne abin da hannayensu suka aikata a duniya, Allah ba ya zaluntar mutane, yana yin hukunci ne tsakaninsu da adalci, shi mai hukunci ne mai adalci.**

**(52) Wannan azabar da ta sauka a kan kafirai ba ta kevanta da su ba, a'a, sunnar Allah ce da ya zartar da ita a kan kafirai a kowane zamani da wuri, haqiqa (Irin wannan azaba) ta samu mabiya Fir'auna da al'ummun da suke gabaninsu yayin da suka kafirce wa ayoyin Allah (S.W.T). Allah ya kama su saboda zunubansu, kamu irin na mai iko da buwaya, ya saukar musu da uqubarsa. Haqiqa Allah mai qarfi ne, ba a rinjayarsa, ba a fin qarfinsa, kuma mai tsananin uquba ne ga wanda ya sava masa.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Girman kai da ji-da-isa yana rushe ginin halittar mutum, kuma yana gaggauta ruguza ma'abocinsa. 2 - Haquri yana taimaka wa wajen xaukan tsanani da wahalhalu, kuma haquri yana da amfani, shi ne taimakon da Allah yake ba wanda ya yi haquri wajen kamanta umarninsa, wannan abu ne da an gan shi a wannan rayuwa ta duniya. 3 - Jayayya da Sassavawa suna cikin dalilan rabuwar al'umma, kuma alamun da suke nuna za a ci nasara a kanta, da nuna cin bayanta, da tafiyar qarfinta, da daularta. 4 - Imani yana wajabta wa ma'abocinsa shiga cikin abubuwan ban tsoro, waxanda runduna masu girma basa iya afkawa cikinsu.**

ذَٰلِكَ بِأَنَّ ٱللَّهَ لَمۡ يَكُ مُغَيِّرٗا نِّعۡمَةً أَنۡعَمَهَا عَلَىٰ قَوۡمٍ حَتَّىٰ
يُغَيِّرُواْ مَا بِأَنفُسِهِمۡ وَأَنَّ ٱللَّهَ سَمِيعٌ عَلِيمٞ ٥٣ كَدَأۡبِ ءَالِ
فِرۡعَوۡنَ وَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡۚ كَذَّبُواْ بِـَٔايَٰتِ رَبِّهِمۡ فَأَهۡلَكۡنَٰهُم
بِذُنُوبِهِمۡ وَأَغۡرَقۡنَآ ءَالَ فِرۡعَوۡنَۚ وَكُلّٞ كَانُواْ ظَٰلِمِينَ ٥٤
إِنَّ شَرَّ ٱلدَّوَآبِّ عِندَ ٱللَّهِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ فَهُمۡ لَا يُؤۡمِنُونَ
٥٥ ٱلَّذِينَ عَٰهَدتَّ مِنۡهُمۡ ثُمَّ يَنقُضُونَ عَهۡدَهُمۡ فِي كُلِّ
مَرَّةٖ وَهُمۡ لَا يَتَّقُونَ ٥٦ فَإِمَّا تَثۡقَفَنَّهُمۡ فِي ٱلۡحَرۡبِ فَشَرِّدۡ بِهِم
مَّنۡ خَلۡفَهُمۡ لَعَلَّهُمۡ يَذَّكَّرُونَ ٥٧ وَإِمَّا تَخَافَنَّ مِن قَوۡمٍ
خِيَانَةٗ فَٱنۢبِذۡ إِلَيۡهِمۡ عَلَىٰ سَوَآءٍۚ إِنَّ ٱللَّهَ لَا يُحِبُّ ٱلۡخَآئِنِينَ
٥٨ وَلَا يَحۡسَبَنَّ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ سَبَقُوٓاْۚ إِنَّهُمۡ لَا يُعۡجِزُونَ
٥٩ وَأَعِدُّواْ لَهُم مَّا ٱسۡتَطَعۡتُم مِّن قُوَّةٖ وَمِن رِّبَاطِ ٱلۡخَيۡلِ
تُرۡهِبُونَ بِهِۦ عَدُوَّ ٱللَّهِ وَعَدُوَّكُمۡ وَءَاخَرِينَ مِن دُونِهِمۡ
لَا تَعۡلَمُونَهُمُ ٱللَّهُ يَعۡلَمُهُمۡۚ وَمَا تُنفِقُواْ مِن شَيۡءٖ فِي سَبِيلِ
ربع الحزب ١٩ ٱللَّهِ يُوَفَّ إِلَيۡكُمۡ وَأَنتُمۡ لَا تُظۡلَمُونَ ٦٠ ۞ وَإِن جَنَحُواْ لِلسَّلۡمِ
فَٱجۡنَحۡ لَهَا وَتَوَكَّلۡ عَلَى ٱللَّهِ إِنَّهُۥ هُوَ ٱلسَّمِيعُ ٱلۡعَلِيمُ ٦١



**(53) An yi musu wannan uquba mai tsanani ne, saboda idan Allah ya yi wa mutane ni'ima, to ba zai canza ta ba, har sai sun canza da kansu, daga hali nagari, na imani da tsayuwa kan addini da gode wa ni'imar Allah, zuwa mummunan hali na kafirci da Allah, da sava masa, da butulce wa ni'imarsa. Kuma tabbas Allah yana jin maganganun bayinsa, yana kuma sane da ayyukansu, babu abin da yake vuya a gare shi.**
**(54) Sha'anin waxannan kafirai kamar sha'anin waninsu ne, daga cikin waxanda suke kafirce wa Allah, kamar mabiya Fir'auna da al'ummun da suka qaryata a gabaninsu, sun qaryata ayoyin Ubangijinsu, sai Allah ya halakar da su saboda abin da suka aikata na savo, ya halakar da mabiya Fir'auna da nutsewa a cikin kogi. Dukkaninsu, mabiya Fir'auna da al'ummun da suke gabaninsu, sun kasance azzalumai saboda kafircewarsu ga Allah, da haxa shi da wani a cikin ibada (Wato shirka), don haka sai suka cancanci uquba daga, don haka sai Allah ya jefa musu ita.**
**(55) Mafi sharrin wanda yake tafiya a bayan qasa, su ne waxanda suka kafirce wa Allah da Manzanninsa, basa yin imani, koda duk wata aya ta zo musu, saboda togewarsu a kan kafirci, duk wata hanyar shiriyarsu ta lalace, tun daga hankali da ji, da gani.**
**(56) Waxanda ka qulla alqawura da yarjejjeniya da su – kamar Bani-Quraiza – sannan suka warware abin da kuka yi alqawari a kai, a kowane lokaci, alhali su basa tsoron Allah, basa cika alqawuransu, basa lazimtar alqawuran da suka xauka. (57) Ya kai wannan Manzo idan ka haxu da waxannan masu warware alqawuransu a wurin yaqi, ka yi musu azaba mai tsanani, har sauran mutane su ji labarin hakan, ko sa xau izina daga abin da ya sami waxancan, sai su ji tsoron yaqarka, da taimakon maqiyanka a kanka. (58) Ya kai wannan Manzo idan ka ji tsoron yaudara da algush da warware alqawari, daga wasu mutane, da ka qulla alqawari da su, saboda wata alama da ta bayyana gare ka, to ka sanar da su warware wannan alqawarin, don ku yi daidai wajen sanin hakan, kada ka afka musu, kafin su sani, afka musu kafin sanar da su yana daga cikin cin amana, kuma Allah baya son masu cin amana, yana qin su, don haka ka kiyayi cin amana da ha'inci. (59) Kada waxanda suka kafirta su yi zaton sun kuvuta daga uqubar Allah, sun kubce masa, tabbas su baza su kubce masa ba, kuma baza su kuvuta ba, zai riske su, zai kama su.**
**(60) Yaku muminai ku tanadi abin da zaku iya tanadarsa, na adadi da shiri, kamar koyon jifa da mashi. Haka nan ku tanadi dawakan da zaku xaure saboda Allah, waxanda zaku tsorata maqiyan Allah, maqiyanku daga cikin kafirai da su, kafiran da suke jiran musifa ta faxa muku, haka kuma don ku tsorata wasu mutanen daban da su, waxanda baku san su ba, baku san abin da suke voye muku na qiyayya ba, Allah ne kaxai ya san su, ya san abin da suke voye wa a zukatansu. Duk abin da kuka ciyar na dukiya, kaxan ne ko da yawa, Allah zai ba ku madadinsa a duniya, ya ba ku ladansa cikakke ba tauyewa a lahira, don haka ku yi gaggawa zuwa ga ciyarwa a kan tafarkinsa.**
**(61) Idan sun karkata zuwa ga sulhu, da barin yaqi, to kai ma ka karkata zuwa ga hakan, ka qulla alqawari da su, ka dogara ga Allah, ka yarda da shi, ba zai tavar da kai ba, Haqiqa Allah mai jin maganganunsu ne, kuma Masani ne ga niyyoyinsu da ayyukansu.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - Daga cikin fa'idodin uquba da haddi da a ka yi saboda wani savo, ya kan zama tsoratarwa ga wanda bai aikata savon ba, kamar yadda yake tsawatar wa ga wanda ya aikata, ba zai qara ba. 2 - Yana daga cikin halayen mumini cika alqawari ga waxanda suka cika musu alqawari, sai dai in sun samu tabbacin cin amana daga gare su. 3 - Wajibi ne a kan musulmi su tanadi duk abin da zai tsoratar da maqiyi, na makami da ra'ayi da shugabanci. 4 - Halaccin yin sulhu da abokin gaba, idan akwai maslahar musulmi a ciki.**

وَإِن يُرِيدُوٓاْ أَن يَخۡدَعُوكَ فَإِنَّ حَسۡبَكَ ٱللَّهُۚ هُوَ ٱلَّذِيٓ أَيَّدَكَ
بِنَصۡرِهِۦ وَبِٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٢ وَأَلَّفَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡۚ لَوۡ أَنفَقۡتَ
مَا فِي ٱلۡأَرۡضِ جَمِيعٗا مَّآ أَلَّفۡتَ بَيۡنَ قُلُوبِهِمۡ وَلَٰكِنَّ ٱللَّهَ
أَلَّفَ بَيۡنَهُمۡۚ إِنَّهُۥ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٦٣ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَسۡبُكَ
ٱللَّهُ وَمَنِ ٱتَّبَعَكَ مِنَ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ ٦٤ يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ حَرِّضِ
ٱلۡمُؤۡمِنِينَ عَلَى ٱلۡقِتَالِۚ إِن يَكُن مِّنكُمۡ عِشۡرُونَ صَٰبِرُونَ
يَغۡلِبُواْ مِاْئَتَيۡنِۚ وَإِن يَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ يَغۡلِبُوٓاْ أَلۡفٗا مِّنَ
ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَفۡقَهُونَ ٦٥ ٱلۡـَٰٔنَ خَفَّفَ
ٱللَّهُ عَنكُمۡ وَعَلِمَ أَنَّ فِيكُمۡ ضَعۡفٗاۚ فَإِن يَكُن مِّنكُم مِّاْئَةٞ
صَابِرَةٞ يَغۡلِبُواْ مِاْئَتَيۡنِۚ وَإِن يَكُن مِّنكُمۡ أَلۡفٞ يَغۡلِبُوٓاْ
أَلۡفَيۡنِ بِإِذۡنِ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ مَعَ ٱلصَّٰبِرِينَ ٦٦ مَا كَانَ لِنَبِيٍّ
أَن يَكُونَ لَهُۥٓ أَسۡرَىٰ حَتَّىٰ يُثۡخِنَ فِي ٱلۡأَرۡضِۚ تُرِيدُونَ عَرَضَ
ٱلدُّنۡيَا وَٱللَّهُ يُرِيدُ ٱلۡأٓخِرَةَۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٦٧ لَّوۡلَا كِتَٰبٞ
مِّنَ ٱللَّهِ سَبَقَ لَمَسَّكُمۡ فِيمَآ أَخَذۡتُمۡ عَذَابٌ عَظِيمٞ ٦٨ فَكُلُواْ
مِمَّا غَنِمۡتُمۡ حَلَٰلٗا طَيِّبٗاۚ وَٱتَّقُواْ ٱللَّهَۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٦٩



**(62) Ya kai wannan Manzo idan sun yi nufin yaudararka ne da sulhu da barin yaqi, don su shirya yaqarka, to haqiqa Allah ya isar maka makircinsu da yaudararsu, Shi ne wanda ya qarfafa ka da nasararsa, ya qarfafa ka da taimakon da muminai suka yi maka, daga waxanda suka yi hijira da mutanen Madinah.**

**(63) Ya haxa zukatan muminan da ya taimake ka da su, bayan da suna rarrabe, da za ka ciyar da abin da yake bayan qasa na dukiya, don ka haxa zukatansu da suka rarraba, da ba za ka iya haxa su ba, amma Allah Shi kaxai ya haxa tsakaninsu, Haqiqa shi Mabuwayi ne a mulkinsa, ba wanda yake rinjayarsa, Mai hikima ne a cikin qaddarawarsa da tsarinsa da shari'arsa.**

**(64) Ya kai wannan Annabi, haqiqa Allah ya isar maka sharrin maqiyanka, kuma ya isar wa muminan da suke tare da kai, don haka ka aminta da Allah, ka dogara gare shi.**

**(65) Ya kai wannan Annabi ka kwaxaitar da muminai a kan yaqi, ka kwaxaitar da su a kanshi, da abin da zai qara musu azama, ya qara nishaxi a himmarsu. Idan a cikinku – Ya ku muminai – a ka samu mutum ishirin masu haquri akan yaqar kafirai, za su rinjayi kafirai xari biyu. Idan aka samu mutum xari masu haquri, za su rinjayi kafirai dubu, saboda kafirai mutane ne da basa fahimtar sunnar Allah, wajen taimakon waliyyansa, da daqile maqiyansa, basa gane manufar yaqi, kawai suna yin yaqin ne don neman xaukaka a duniya.**

**(66) Yanzu Allah ya sauwaqa muku – Ya ku muminai – saboda abin da ya sani na rauninku, da tausayinsa gare ku, don haka ya wajabta wa kowane xaya daga cikinku ya tabbata a gaban mutum biyu daga kafirai, maimakon goma, don haka idan ya kasance a cikinku akwai mutum xari masu haquri a kan yaqin kafirai, to zasu rinjayi kafirai xari biyu, idan aka samu mutum dubu masu haquri, zasu rinjayi dubu biyu, daga kafirai, da izinin Allah. Allah yana tare da masu haquri, daga cikin muminai, yana ba su nasara, yana qarfafa su. (67) Bai dace ga Annabi ba, ya zama yana da ribatattun yaqi daga cikin kafirai, waxanda suke yaqarsa, har sai ya zubar da jininsu, don ya shigar da tsoro a cikin zukatansu, don kada su qara dawowa zuwa ga yaqarsa, amma ku muminai kuna son karvar fansa ta hanyar riqe ribatattun yaqin, Allah kuma yana nufin lahira ne, wadda ake samunta ta hanyar taimakon addini da xaukaka shi. Allah Mabuwayi ne a cikin zatinsa da siffofinsa, da qarfinsa, ba wanda yake rinjayarsa, mai hikima ne a cikin abin da ya tsara da shari'arsa.**

**(68) Ba don littafin Allah na hukuncinsa da tsarinsa ( wato qaddararsa) da ya riga ya gabata ba, na halatta muku ganima, da halatta muku karvar fansar ribatattu, da azaba mai tsanani daga Allah ta same ku, saboda abin da kuka karva na ganima da fansar ribatattu, tun kafin wahayi ya sauka daga wajen Allah na halaccin hakan.**

**(69) Yaku muminai ku ci daga abin da kuka karva daga kafirai na ganima, halal ne gare ku. Ku ji tsoron Allah ta hanyar kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana, haqiqa Allah mai yawan gafara ne ga bayinsa, mai jinqai ne gare su.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - A cikin waxannan ayoyi Allah ya yi wa bayinsa muminai alqawarin isar musu daga duk wani abokin gaba, da ba su nasara a kan maqiya.**

**2 - Tsayawa da tabbata a gaban maqiyi farilla ne a kan musulmi, ba su da wani zavi a kan hakan, matuqar abin da zai sa a yi musu rangwame bai faru ba. 3 - Allah yana so wa bayinsa al'amura masu girma, kuma yana qi musu maqasqantan al'amura, don haka ya kwaxaitar da su a kan neman ladan lahira, mai dauwama da wanzuwa.**

**4 - Ba da fansar ribatattun yaqi, ko yi musu baiwa ta sakinsu, hakan baya faruwa sai bayan samun nasara da iko a kan maqiya, da bayyanar kwarjinin daula a gaban waxanda ba musulmi ba.**

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ قُل لِّمَن فِيٓ أَيۡدِيكُم مِّنَ ٱلۡأَسۡرَىٰٓ إِن يَعۡلَمِ ٱللَّهُ
فِي قُلُوبِكُمۡ خَيۡرٗا يُؤۡتِكُمۡ خَيۡرٗا مِّمَّآ أُخِذَ مِنكُمۡ وَيَغۡفِرۡ لَكُمۡۚ
وَٱللَّهُ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٧٠ وَإِن يُرِيدُواْ خِيَانَتَكَ فَقَدۡ خَانُواْ ٱللَّهَ
مِن قَبۡلُ فَأَمۡكَنَ مِنۡهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ٧١ إِنَّ ٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡ فِي سَبِيلِ
ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ وَٱلَّذِينَ
ءَامَنُواْ وَلَمۡ يُهَاجِرُواْ مَا لَكُم مِّن وَلَٰيَتِهِم مِّن شَيۡءٍ حَتَّىٰ يُهَاجِرُواْۚ
وَإِنِ ٱسۡتَنصَرُوكُمۡ فِي ٱلدِّينِ فَعَلَيۡكُمُ ٱلنَّصۡرُ إِلَّا عَلَىٰ قَوۡمِۭ
بَيۡنَكُمۡ وَبَيۡنَهُم مِّيثَٰقٞۗ وَٱللَّهُ بِمَا تَعۡمَلُونَ بَصِيرٞ ٧٢ وَٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ بَعۡضُهُمۡ أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٍۚ إِلَّا تَفۡعَلُوهُ تَكُن فِتۡنَةٞ فِي
ٱلۡأَرۡضِ وَفَسَادٞ كَبِيرٞ ٧٣ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ
فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱلَّذِينَ ءَاوَواْ وَّنَصَرُوٓاْ أُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ
حَقّٗاۚ لَّهُم مَّغۡفِرَةٞ وَرِزۡقٞ كَرِيمٞ ٧٤ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مِنۢ بَعۡدُ
وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ مَعَكُمۡ فَأُوْلَٰٓئِكَ مِنكُمۡۚ وَأُوْلُواْ ٱلۡأَرۡحَامِ
بَعۡضُهُمۡ أَوۡلَىٰ بِبَعۡضٖ فِي كِتَٰبِ ٱللَّهِۚ إِنَّ ٱللَّهَ بِكُلِّ شَيۡءٍ عَلِيمُۢ ٧٥



**(70) Ya kai wannan Annabi ka ce wa waxanda suka faxa hannunku daga ribatattun mushirikai, waxanda kuka kama a ranar yaqin Badar, ka ce da su: "In Allah ya san nufin alheri ne a zuciyarku, kuna da niyya mai kyau, to zai baku mafi alherin abin da aka karva daga gareku na fansa, don haka kada ku yi baqin ciki a kan abin da aka karva a wurinku, kuma zai gafarta muku zunubanku, Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jinqansu ne. Tabbas wannan alqawarin da Allah ya yi, ya tabbata a kan Abbas baffan Annabi (S.A.W) da abokansa, daga cikin waxanda suka musulunta daga baya.**

**(71) Idan kuwa sun yi nufin ha'intarka ne – Ya kai wannan Annabi – da abin da suka bayyana maka na magana, to dama sun ha'inci Allah ma tun gabanin hakan, kuma duk da haka Allah ya baka nasara a kansu, aka kashe wanda aka kashe a cikinsu, aka kama wanda aka kama, don haka su saurari kwatankwancin hakan idan sun sake aikata hakan. Allah Masani ne da halittarsa, ya san abin da zai gyara su, kuma mai hikima ne a cikin tsarinsa.**

**(72) Haqiqa waxanda suka yi imani da Allah, suka gasgata Manzonsa, suka yi aiki da shari'arsa, suka yi hijira daga garin kafirci zuwa garin musulunci, ko zuwa wani wurin da zasu bauta wa Allah cikin aminci da kwanciyar hankali, suka yi jihadi da dukiyarsu, da kawunansu, don xaukaka kalmar Allah, da waxanda suka sauke su a gidajensu, suka taimaki waxanda da suka yi hijira, daga cikin mutanen gari, sashensu masoya sashe ne, a wajen taimakon juna. Waxanda suka yi imani da Allah, basu yi hijira daga garin kafirci zuwa garin musulunci ba, to waxannan babu wajabcin ku taimake su, ko ku kare su, har sai sun yi hijira a kan tafarkin Allah, amma idan kafirai suka zalunce su, suka nemi taimakonku to ku taimake su a kan maqiyansu, sai dai idan tsakaninku da maqiyan nasu akwai alqawarin da ba su warware shi ba. Allah yana ganin abin da kuke aikata wa, babu abin da yake vuya gare shi, daga ayyukanku, kuma zai ba da sakamako a kansu.**

**(73) Waxanda suka kafirta da Allah, to kafirci ya haxa su, don sashensu yana taimakon sashe, kada mumini ya so su, kuma idan ba ku so muminai ba, ba ku qi kafirai ba, to za a samu fitina ga muminai, ta inda za su rasa wanda zai taimake su daga 'yan uwansu na addini, don haka varna mai yawa za ta kasance a bayan qasa, ta hanyar kange mutane daga tafarkin Allah.**

**(74) Waxanda suka yi imani da Allah, suka yi hijira a kan tafarkinsa, da waxanda suka tattaro waxanda suka yi hijira saboda Allah, suka taimake su, waxannan su ne suka siffatu da imani na gaskiya, suna da duk haqqin da kuke da shi, kuma duk abin da yake kanku na wajibai yana kansu. Ma'abota kusanci (wato yan uwa na jini) a cikin hukuncin Allah sashensu yafi cancanta da sashe a wajen gado, fiye da cin gado a kan imani da hijira, wanda kuke yi a da. Haqiqa Allah masanin dukkan komai ne, babu abin da yake vuya a gare shi, ya san abin da zai gyara bayinsa, don haka ya shar'anta musu shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Karantarwa:

**1 - Wajibi ne a kan muminai su kwaxaitar da ribatattu a kan su yi imani da Allah.**

**2 - Ayoyin sun qunshi bushara ga muminai da samun ci gaba da nasara a kan mushirikai, matuqar suna riqe da sabubban nasara na fili da na voye.**

**3 - Idan musulmi ba su zama hannu xaya a kan kafirai ba, to qarfinsu ba zai bayyana ba, kuma sai varna mai yawa ta faru saboda hakan.**

**4 - Falalar cika alqawura da yarjajjeniya a shari'ar musulunci, ko da kuwa hakan ya ci karo da maslahar musulmai.**

سُورَةُ التَّوبَةِ

آياتها ١٢٩ — ترتيبها ٩

نصف الحزب ١٩

بَرَآءَةٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ إِلَى ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ١
فَسِيحُواْ فِي ٱلۡأَرۡضِ أَرۡبَعَةَ أَشۡهُرٖ وَٱعۡلَمُوٓاْ أَنَّكُمۡ غَيۡرُ مُعۡجِزِي
ٱللَّهِ وَأَنَّ ٱللَّهَ مُخۡزِي ٱلۡكَٰفِرِينَ ٢ وَأَذَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦٓ
إِلَى ٱلنَّاسِ يَوۡمَ ٱلۡحَجِّ ٱلۡأَكۡبَرِ أَنَّ ٱللَّهَ بَرِيٓءٞ مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ
وَرَسُولُهُۥۚ فَإِن تُبۡتُمۡ فَهُوَ خَيۡرٞ لَّكُمۡۖ وَإِن تَوَلَّيۡتُمۡ فَٱعۡلَمُوٓاْ
أَنَّكُمۡ غَيۡرُ مُعۡجِزِي ٱللَّهِۗ وَبَشِّرِ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ بِعَذَابٍ أَلِيمٍ
٣ إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّم مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ثُمَّ لَمۡ يَنقُصُوكُمۡ شَيۡـٔٗا
وَلَمۡ يُظَٰهِرُواْ عَلَيۡكُمۡ أَحَدٗا فَأَتِمُّوٓاْ إِلَيۡهِمۡ عَهۡدَهُمۡ إِلَىٰ مُدَّتِهِمۡۚ
إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ٤ فَإِذَا ٱنسَلَخَ ٱلۡأَشۡهُرُ ٱلۡحُرُمُ
فَٱقۡتُلُواْ ٱلۡمُشۡرِكِينَ حَيۡثُ وَجَدتُّمُوهُمۡ وَخُذُوهُمۡ وَٱحۡصُرُوهُمۡ
وَٱقۡعُدُواْ لَهُمۡ كُلَّ مَرۡصَدٖۚ فَإِن تَابُواْ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ
ٱلزَّكَوٰةَ فَخَلُّواْ سَبِيلَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٥ وَإِنۡ أَحَدٞ
مِّنَ ٱلۡمُشۡرِكِينَ ٱسۡتَجَارَكَ فَأَجِرۡهُ حَتَّىٰ يَسۡمَعَ كَلَٰمَ
ٱللَّهِ ثُمَّ أَبۡلِغۡهُ مَأۡمَنَهُۥۚ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمۡ قَوۡمٞ لَّا يَعۡلَمُونَ ٦



# Suratut Tauba

An Saukar Da Ita A Madinah

## Daga Manufofin Surar:

**Bayyana halin mutane dangane da alaqarsu da kafirai, da fallasa munafukai, sannan da tantance muminai na gaskiya.**

## Tafsiri:

**(1) Wannan (sanarwar ce) ta barranta daga wajen Allah da Manzonsa, da sanar da qarewar alqawuran da kuka qulla tsakaninku – ku musulmai – da mushirikai a jazirar larabawa. (2) Ya ku mushirikai ku yi tafiya a bayan qasa tsawon wata huxu, kuna cikin aminci, amma babu alqawari da yarjejjeniya da aminci bayansu, idan kuka ci gaba da kafirce wa Allah to ku tabbatar ba za ku kubcewa azabarsa da uqubarsa ba, ku tabbas Allah mai qasqanta kafirai ne, ta hanyar kisa da kamu a duniya, da shiga wuta a ranar alqiyama. Wannan (damar da aka ba su ta yawo tsawon wata huxu a cikin aminci, da janye aminci da alqawari bayan wucewarsu) ya haxa da waxanda suka warware alqawarinsu, da waxanda alqawarinsu yake sakakke ba shi da lokaci. Amma wanda ake da yarjejjeniya da alqawari da su zuwa wani lokaci, to shi za a cika musu alqawarinsu zuwa lokacin da aka yi da su. (3) Sanarwa daga Allah da Manzonsa, zuwa ga dukkan mutane a ranar yanka (wato ranar sallah) cewa haqiqa Allah (S.W.T) ya barranta daga mushirikai, haka ma manzonsa shi ma ya barranta daga mushirikai. Idan kun tuba - Ya ku mushirikai – daga shirkar da kuke yi, to tubanku ya fi alheri gare ku, idan kuwa kuka bijire daga tuba, to ku tabbatar baza ku kubcewa Allah ba, ba za ku kubcewa uqubarsa ba. Ka ba wa waxanda suka kafirce wa Allah labarin da zai baqanta musu rai – Ya kai wannan manzo -, shi ne labarin azaba mai ciwo da take jiransu. (4) Sai waxanda kuka yi yarjejjeniya da alqawari da su daga mushirikai, suka cika alqawarinsu, basu warware komai ba, to su an kevance su daga wancan hukunci da ya gabata, ku cika musu alqawarinsu, har lokacinsu ya qare. Haqiqa Allah yana son masu tsoronsa, ta hanyar kamanta umarninsa, wanda daga cikinsu akwai cika alqawari, da nisantar abubuwan da ya hana, wanda daga cikinsu akwai ha'inci da cin amana. (5) Idan watanni masu alfarma suka qare, waxanda kuka amintar da maqiyanku a cikinsu, to ku yaqi mushirikai a duk inda kuka gamu da su, ku kewaye su a inda suke, ku yi dakonsu a hanyoyinsu, idan sun tuba zuwa ga Allah, suka bar shirka, suka tsaida sallah, suka ba da zakkar dukiyoyinsu, to sun zama 'yan uwanku a musulunci, ku daina yaqarsu. Haqiqa Allah mai yawan gafara ne ga wanda ya tuba daga cikin bayinsa, mai jinqansa ne. (6) Idan wani mushiriki wanda jininsa da dukiyarsa suka halatta ya shigo neman mafaka a wurinka – Ya wannan manzo – to ka amsa masa abin da ya nema, har ya ji karatun Alqur'ani, sannan sai ka isar da shi zuwa wurin da zai samu aminci a cikinsa, saboda kafirai mutane ne da ba su san haqiqanin wannan addini ba, idan suka san shi ta hanyar jin Alqur'ani, wataqila su shiriya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - A cikin waxannan ayoyin akwai dalili bayyananne a kan kwaxayin musulunci a kan daidata alaqa da maqiya, a kan tushen aminci da zaman lafiya, da fahimta. 2 - Musulunci yana girmama alqawura da yarjejjeniya, don haka ya wajabta cika su, da kiyaye su, kuma ya sanya hakan wani abu ne da yake fitowa daga imani, da lazimtar tsoron Allah Maxaukakin Sarki.**

**3 - Tsaida sallah da bayar da zakka, dalili ne da yake nuna musulunci, kuma yin su yana kare jini da dukiya, yana wajabta haqqoqin musulunci a kan wanda yake yin su, na kiyaye jininsa da dukiyarsa, sai da haqqin musulunci, kamar aikata abin da yake wajabta kisa, kamar kashe ran da ba ruwanta, da zina daga bazawari, da komawa kafirci bayan imani. 4 - Halaccin amintar da kafirin da ake yaqi da shi, idan ya nemi hakan a wurin musulmi, don ya ji abin da zai nuna masa ingancin musulunci. A cikin wannan akwai rangwame da girmama mu'amalar kafirai, da fifita zaman lafiya da aminci.**

كَيۡفَ يَكُونُ لِلۡمُشۡرِكِينَ عَهۡدٌ عِندَ ٱللَّهِ وَعِندَ رَسُولِهِۦٓ
إِلَّا ٱلَّذِينَ عَٰهَدتُّمۡ عِندَ ٱلۡمَسۡجِدِ ٱلۡحَرَامِۖ فَمَا ٱسۡتَقَٰمُواْ
لَكُمۡ فَٱسۡتَقِيمُواْ لَهُمۡۚ إِنَّ ٱللَّهَ يُحِبُّ ٱلۡمُتَّقِينَ ٧
كَيۡفَ وَإِن يَظۡهَرُواْ عَلَيۡكُمۡ لَا يَرۡقُبُواْ فِيكُمۡ إِلّٗا وَلَا
ذِمَّةٗۚ يُرۡضُونَكُم بِأَفۡوَٰهِهِمۡ وَتَأۡبَىٰ قُلُوبُهُمۡ وَأَكۡثَرُهُمۡ
فَٰسِقُونَ ٨ ٱشۡتَرَوۡاْ بِـَٔايَٰتِ ٱللَّهِ ثَمَنٗا قَلِيلٗا فَصَدُّواْ عَن
سَبِيلِهِۦٓۚ إِنَّهُمۡ سَآءَ مَا كَانُواْ يَعۡمَلُونَ ٩ لَا يَرۡقُبُونَ
فِي مُؤۡمِنٍ إِلّٗا وَلَا ذِمَّةٗۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡمُعۡتَدُونَ ١٠ فَإِن
تَابُواْ وَأَقَامُواْ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَوُاْ ٱلزَّكَوٰةَ فَإِخۡوَٰنُكُمۡ فِي
ٱلدِّينِۗ وَنُفَصِّلُ ٱلۡأٓيَٰتِ لِقَوۡمٖ يَعۡلَمُونَ ١١ وَإِن
نَّكَثُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُم مِّنۢ بَعۡدِ عَهۡدِهِمۡ وَطَعَنُواْ فِي دِينِكُمۡ
فَقَٰتِلُوٓاْ أَئِمَّةَ ٱلۡكُفۡرِ إِنَّهُمۡ لَآ أَيۡمَٰنَ لَهُمۡ لَعَلَّهُمۡ
يَنتَهُونَ ١٢ أَلَا تُقَٰتِلُونَ قَوۡمٗا نَّكَثُوٓاْ أَيۡمَٰنَهُمۡ
وَهَمُّواْ بِإِخۡرَاجِ ٱلرَّسُولِ وَهُم بَدَءُوكُمۡ أَوَّلَ مَرَّةٍۚ
أَتَخۡشَوۡنَهُمۡۚ فَٱللَّهُ أَحَقُّ أَن تَخۡشَوۡهُ إِن كُنتُم مُّؤۡمِنِينَ ١٣



**(7) Ba zai yi wu ba, a ce mushirikai masu haxa Allah da wani suna da alqawari da aminci a wurin Allah da Manzonsa, sai dai alqawarin waxancan mushirikai wanda kuka qulla da su – Ya ku musulmi – a wajen masallaci mai alfarma (Harami) a Hudaibiyyah. Idan sun tsaya muku a kan alqawarin da yake tsakaninku da su, basu warware shi ba, to kuma ku tsaya a kan abin da kuke kai, kada ku warware shi. Haqiqa Allah yana son masu tsoronsa daga cikin bayinsa, waxanda suke kamanta umarninsa, da nisantar abubuwan da ya hana.**

**(8) Ta yaya zai kasance suna da alqawari da aminci alhali su maqiyanku ne, idan kuma suka samu dama a kanku basa duba Allah ko kusanci ko alqawarin da yake tsakaninku, kawai, za su xanxana muku azaba mai tsanani ne? Suna neman yardarku da magana mai kyau, wadda harshensu yake faxa, amma basa cika abin da suke faxa,kuma mafi yawancinsu masu fita ne daga xa'ar Allah, ta hanyar warware alqawarinsu.**

**(9) Sun canza bin ayoyin Allah, waxanda a cikinsu akwai cika alqawura, sun canza su da kuxi wulaqantacce, na daga abubuwan duniya, waxanda suke biyan sha'awarsu da son zuciyarsu da su, sai suka kange kawunansu daga bin gaskiya. Tir da aikinsu da suke aikatawa.**

**(10) Basa duban Allah ko kusanci ko alqawari dangane da mumini, saboda abin da suke kai na gaba, suna qetare iyakokin Allah, saboda abin da suka siffatu da shi na zalunci da varna.**

**(11) Idan sun tuba daga kafircinsu zuwa ga Allah, suka faxi kalmar shahada, suka tsaida sallah, suka bada zakkar dukiyoyinsu, to sun zama musulmi, su 'yan uwanku ne a addini, duk abin da kuke da shi na haqqi, su ma suna da shi, haka abin da yake kanku yana kansu, baya halatta su yaqe su, musuluncinsu ya tsare jininsu da dukiyoyinsu da mutuncinsu. Muna bayyana ayoyi ga mutanen da suka da ilimi, su ne suke amfanu wa da su, kuma suke amfanar da waninsu da ita.**

**(12) Idan waxannan mushirikai suka warware abin da suka yi muku alqawari na barin yaqi, tsawon lokacin alqawarinsu da yarjejjeniyarsu, suka aibata addininku, suka tauye shi, ku yaqe su, don su jagororin kafirci ne, basu da wani alqawari, ba su da wata yarjejjeniya da zata tsare jininsu, don haka ku yaqe su, ko sa bar kafircinsu da warware alqawuransu da tauye addini.**

**(13) Don me – Ya ku muminai – baza ku yaqi mutanen da suka warware alqawuransu da yarjejjeniyarsu ba, suka yi gaggawar taruwa a gidan Nadwa don fitar da Manzo (S.A.W) daga Makkah, kuma su suka fara yaqarku a farkon lamari, suka taimaki qabilar bakra, abokiyar qabilar Quraishawa, a kan qabilar Khuza'a abokiyar Manzon Allah (S.A.W). kuna jin tsoronsu ne da baza ku tunkare su da yaqi ba? Allah tsarki ya tabbata a gare shi, shi ne ya fi cancanta ku ji tsoronsa, indai ku muminai ne na gaskiya.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Ayoyin sun nuna yaqar mushirikai, waxanda suka warware alqawura, ya faru ne saboda abubuwa da yawa, mafi mahimmancinsu: warware alqawura.**

**2 - A cikin ayoyin akwai dalili a kan duk wanda ya qi yin sallah, ya qi bayar da zakkah, to za a yaqe shi, har sai ya yi su, kamar yadda Sayyidina Abubukar (R.A) ya aikata.**

**3 - Wasu malamai sun kafa hujja da faxin Allah (Suka soki addininku) a kan wajabcin kashe duk wanda ya soki addini da gangan, yana mai izgili da shi.**

**4 - A cikin ayoyin akwai dalili a kan muminin da Allah kaxai yake tsoro, ya zama ya fi dukkan mutane jaruntaka, da qarfin shiga yaqi.**

قَٰتِلُوهُمۡ يُعَذِّبۡهُمُ ٱللَّهُ بِأَيۡدِيكُمۡ وَيُخۡزِهِمۡ وَيَنصُرۡكُمۡ
عَلَيۡهِمۡ وَيَشۡفِ صُدُورَ قَوۡمٖ مُّؤۡمِنِينَ ١٤ وَيُذۡهِبۡ غَيۡظَ
قُلُوبِهِمۡۗ وَيَتُوبُ ٱللَّهُ عَلَىٰ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٌ ١٥
أَمۡ حَسِبۡتُمۡ أَن تُتۡرَكُواْ وَلَمَّا يَعۡلَمِ ٱللَّهُ ٱلَّذِينَ جَٰهَدُواْ مِنكُمۡ
وَلَمۡ يَتَّخِذُواْ مِن دُونِ ٱللَّهِ وَلَا رَسُولِهِۦ وَلَا ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَلِيجَةٗۚ
وَٱللَّهُ خَبِيرُۢ بِمَا تَعۡمَلُونَ ١٦ مَا كَانَ لِلۡمُشۡرِكِينَ أَن يَعۡمُرُواْ مَسَٰجِدَ
ٱللَّهِ شَٰهِدِينَ عَلَىٰٓ أَنفُسِهِم بِٱلۡكُفۡرِۚ أُوْلَٰٓئِكَ حَبِطَتۡ
أَعۡمَٰلُهُمۡ وَفِي ٱلنَّارِ هُمۡ خَٰلِدُونَ ١٧ إِنَّمَا يَعۡمُرُ مَسَٰجِدَ
ٱللَّهِ مَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَأَقَامَ ٱلصَّلَوٰةَ وَءَاتَى
ٱلزَّكَوٰةَ وَلَمۡ يَخۡشَ إِلَّا ٱللَّهَۖ فَعَسَىٰٓ أُوْلَٰٓئِكَ أَن يَكُونُواْ مِنَ
ثلاثة أرباع الحزب ١٩ ٱلۡمُهۡتَدِينَ ١٨ ۞أَجَعَلۡتُمۡ سِقَايَةَ ٱلۡحَآجِّ وَعِمَارَةَ ٱلۡمَسۡجِدِ
ٱلۡحَرَامِ كَمَنۡ ءَامَنَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَجَٰهَدَ فِي سَبِيلِ
ٱللَّهِۚ لَا يَسۡتَوُۥنَ عِندَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلظَّٰلِمِينَ
١٩ ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ وَهَاجَرُواْ وَجَٰهَدُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ
وَأَنفُسِهِمۡ أَعۡظَمُ دَرَجَةً عِندَ ٱللَّهِۚ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡفَآئِزُونَ ٢٠



**(14) Yaku muminai ku yaqi waxannan mushirikai, idan kuka yaqe su Allah zai azabtar da su da hannunku, ta hanyar kashe su da zaku yi, ya qasqantar da su da rashin cin nasara da kamu, ya taimake ku a kansu, ya baku rinjaye, ya warkar da cutar da take qirjin muminai, waxanda basu je yaqi ba, da abin da ya samu maqiyansu na kisa da kamu da cin nasara, da samun nasarar muminai.**

**(15) Ya nisantar da baqin ciki daga zukatan bayinsa muminai, da abin da suka samu na nasara a kan kafirai. Allah yana karvar tuban wanda ya ga dama daga cikin waxannan masu taurin kai, idan sun tuba, kamar yadda hakan ya faru ga wasu daga cikin mutanen Makkah, a ranar Fathu Makkah. Allah ya san gaskiyar wanda ya tuba daga cikinsu, kuma mai hikima ne cikin halittarsa da tsarinsa da shar'antawarsa.**

**(16) Yanzu ku muminai kuna zaton Allah ya qyale ku, ba tare da wata jarrabawa ba? Jarrabawa sunna ce daga cikin sunnoninsa, za a jarrabe ku har Allah ya bayyana bayinsa masu jihadi don Allah a cikinku, waxanda basu riqi wasu masoya koma bayan Allah, ko manzonsa, ko muminai ba, abokan shawara daga kafirai suna son su ba, suna qaunarsu. Allah masani ne mai bada labari dangane da abin da kuke aikatawa, babu abin da yake vuya a gare shi, kuma zai saka muku a kan ayyukanku.**

**(17) Bai dace ga mushirikai su raya masallatan Allah da ibada, da sauran ayyukan xa'a ba, alhali sun tabbatar da kafirci ga kawunansu, saboda abin da suka bayyana na waxannan ayyuka. Ayyukansu sun vaci, saboda sun rasa sharaxin da zai sa a karva, wanda shi ne imani, kuma a ranar alqiyama za su shiga wuta, su zauna a cikinta har abada, sai dai in sun tuba daga shirka kafin mutuwarsu.**

**(18) Waxanda kaxai ya cancanta da raya masallatan Allah, shi ne wanda ya yi imani da Allah shi kaxai, kuma bai shirka da shi ba, ya yi imani da ranar alqiyama, ya tsayar da sallah, ya bada zakkar dukiyarsa, bai ji tsoron kowa ba, sai Allah (S.W.T), waxannan su ne waxanda ake fatan su kasance shiryayyu a kan tafarki madaidaici. Amma mushirikai sun fi kowa nisa da hakan.**

**(19) Ya ku Mushirikai kun sanya tsaya wa a kan shayar da alhazai ruwa, da raya masallaci mai alfarma, kamar wanda ya yi imani da Allah, bai yi shirka da shi ba, ya yi imani da ranar alqiyama, ya yi jihadi da ransa da dukiyarsa, don kalmar Allah ta zama ita ce a sama, kuma kalmar waxanda suka kafirta ta zama a qasa, yanzu kun sanya falalarsu xaya a wurin Allah? Ba za su yi daidai ba, har abada a wurin Allah, kuma Allah baya datar da waxanda suka yi zalunci da shirka, koda kuwa suna aikata ayyukan alheri, irin shayar da alhazai ruwa.**

**(20) Waxanda suka haxa imani da Allah da hijira daga garuruwan kafirci zuwa garuruwan musulunci, da jihadi a kan tafarkin Allah, da dukiyoyinsu da rayukansu, sun fi girman daraja a wurin Allah, fiye da waxanda ba su yi hakan ba. Waxanda suka siffatu da waxannan siffofi su ne masu rabauta da Aljannah.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa: 1 - A cikin ayoyin a kwai dalilin da yake nuna Allah yana son bayinsa muminai, yana kula da halayensu, don haka ya sa yana daga cikin manufofin shari'a warkar da abin da yake zukatansu na fushi da damuwa da tafiyar da su.**

**2 - Allah ya shar'anta jihadi don a cimma babbar manufa, ita ce bambance masu gaskiya, waxanda basa yin komai sai addinin Allah, a bambace su daga cikin masu qarya waxanda suke da'awar imani.**

**3 - Masu raya massalatai na haqiqa su ne waxanda aka siffata su da imani na gaskiya, da aikata ayyuka nagartattu, waxanda jagoransu ita ce sallah da zakkah, da tsoron Allah wanda shi ne tushen duk wani alheri.**

**4 - Jihadi da imani da Allah sun fi shayar da alhazai ruwa da raya masallacin harami falala, da darajoji masu girma, saboda imani shi ne tushen addini, jihadi kuwa shi ne qololuwar tozon addini.**

يُبَشِّرُهُمْ رَبُّهُم بِرَحْمَةٍ مِّنْهُ وَرِضْوَانٍ وَجَنَّاتٍ لَّهُمْ فِيهَا
نَعِيمٌ مُّقِيمٌ ﴿٢١﴾ خَالِدِينَ فِيهَا أَبَدًا إِنَّ اللَّهَ عِندَهُ أَجْرٌ
عَظِيمٌ ﴿٢٢﴾ يَا أَيُّهَا الَّذِينَ آمَنُوا لَا تَتَّخِذُوا آبَاءَكُمْ
وَإِخْوَانَكُمْ أَوْلِيَاءَ إِنِ اسْتَحَبُّوا الْكُفْرَ عَلَى الْإِيمَانِ
وَمَن يَتَوَلَّهُم مِّنكُمْ فَأُولَٰئِكَ هُمُ الظَّالِمُونَ ﴿٢٣﴾ قُلْ إِن
كَانَ آبَاؤُكُمْ وَأَبْنَاؤُكُمْ وَإِخْوَانُكُمْ وَأَزْوَاجُكُمْ
وَعَشِيرَتُكُمْ وَأَمْوَالٌ اقْتَرَفْتُمُوهَا وَتِجَارَةٌ تَخْشَوْنَ
كَسَادَهَا وَمَسَاكِنُ تَرْضَوْنَهَا أَحَبَّ إِلَيْكُم مِّنَ اللَّهِ
وَرَسُولِهِ وَجِهَادٍ فِي سَبِيلِهِ فَتَرَبَّصُوا حَتَّىٰ يَأْتِيَ اللَّهُ
بِأَمْرِهِ وَاللَّهُ لَا يَهْدِي الْقَوْمَ الْفَاسِقِينَ ﴿٢٤﴾ لَقَدْ نَصَرَكُمُ
اللَّهُ فِي مَوَاطِنَ كَثِيرَةٍ وَيَوْمَ حُنَيْنٍ إِذْ أَعْجَبَتْكُمْ
كَثْرَتُكُمْ فَلَمْ تُغْنِ عَنكُمْ شَيْئًا وَضَاقَتْ عَلَيْكُمُ
الْأَرْضُ بِمَا رَحُبَتْ ثُمَّ وَلَّيْتُم مُّدْبِرِينَ ﴿٢٥﴾ ثُمَّ أَنزَلَ اللَّهُ
سَكِينَتَهُ عَلَىٰ رَسُولِهِ وَعَلَى الْمُؤْمِنِينَ وَأَنزَلَ جُنُودًا
لَّمْ تَرَوْهَا وَعَذَّبَ الَّذِينَ كَفَرُوا وَذَٰلِكَ جَزَاءُ الْكَافِرِينَ ﴿٢٦﴾



**(21) Ubangijinsu Allah yana ba su labarin da zai faranta musu rai, na ya yi musu rahama, ya yarda da su, kuma ba zai yi fushi da su ba har abada, kuma za su shiga Aljannah, wadda a cikinta akwai dauwamammiyar ni'imar da bata yankewa.**

**(22) Zasu zauna a cikin waxannan Alajannatai, zaman da ba shi da qarshe, don sakamako a kan ayyukansu nagartattu, waxanda suka aikat a duniya. Haqiqa a wajen Allah akwai lada mai girma, ga wanda ya kamanta umarninsa, ya nisanci abubuwan da ya hana, yana mai tsarkake addini gare shi.**

**(23) Ya waxanda suka yi imani da Allah, suka bi abin da Manzonsa ya zo da shi, kada ku mayar da iyayenku da 'yan uwanku na jini da sauransu daga cikin 'yan uwanku masoyanku, kuna qaunarsu, kuna yaxa musu sirrin muminai, kuna shawara da su, matuqar dai sun zavi kafirci a kan imani da Allah shi kaxai. Duk wanda ya mayar da su masoya majivinta lamari, duk da sun zauna a cikin kafirci, amma ya nuna musu qauna, to sun sava wa Allah, kuma wanda ya yi haka ya zalunci kansa, ta hanyar jefa kansa cikin hanyoyin halaka da savo.**

**(24) Ya kai wannan Manzo – ka ce, idan iyayenku – ku muminai – da 'yayanku da 'yan uwanku, da matanku, da makusantanku, da dukiyoyinku, waxanda kuka neme su da ayyukanku, da kasuwancinku, wanda kuke son yaxuwarsa, kuna tsoron lalacewarsa, da gidajenku, waxanda kuka yarda da zama a cikinsu, idan waxannan abubuwa sun fi soyuwa a wurinku fiye da Allah da Manzonsa, da jihadi a kan tafarkin Allah, to ku jira abin da Allah zai saukar muku na uquba da azaba, Allah baya datar da waxanda suka fita daga xa'arsa zuwa ga aikin da ya yarda da shi.**

**(25) Haqiqa Allah ya taimake ku – ku muminai – a kan maqiyanku daga mushirikai a yaqoqi da yawa, duk da qarancin adadinku, da raunin tanadinku, yayin da kuka dogara ga Allah, kuka yi riqo da sabubban samun nasara, baku ruxu da yawanku ba, don yawanku bai tava zama sababin nasararku ba, amma ranar yaqin Hunaini lokacin da yawanku ya qayatar da ku, har kuka ce: "Yau ba za a rinjaye mu ba, saboda qarancinmu, don haka sai yawanku ya qayatar da ku, ya zama bai amfana muku komai ba, maqiyanku suka ci galaba a kanku, qasa ta yi muku qunci, duk da faxinta, sannan kuka juya, kuka gudu ku ka bar maqiyanku, aka ci nasara a kanku.**

**(26) Sannan bayan kun gudu daga maqiyanku, sai Allah ya saukar da nutsuwa ga Manzonsa, ya saukar da ita ga muminai, sai suka tabbata don yin yaqi, kuma ya saukar da Mala'ikun da baku gan su ba, ya azabtar da waxanda suka kafirta, ta hanyar kisa da kamu, da karvar dukiya, da kama zurriya, wannan sakamakon da aka saka wa waxannan da shi, shi ne sakamakon kafirai, masu qaryata manzanninsu, masu bijire wa abin da suka zo da shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Matakan falalar mujahidai yana da yawa, su ne suka fi girman daraja a wurin Allah, fiye da duk wani mai daraja, suna da martaba da xaukaka ta daban, suna masu rabauta, masu tsira, kuma su ne waxanda Ubangijinsu yake musu bushara da ni'ima.**

**2 - A cikin ayoyin akwai babban dalili a kan wajabcin son Allah da Manzonsa, da gabatar da son su a kan son dukkan komai.**

**3 - An kevance ranar Hunai da ambato daga cikin yaqe-yaqen da aka yi, saboda abin da ya faru a wannan rana, na izina, da samuwar nasara yayin da a ka kamanta umarnin Allah da Manzonsa, da kuma rashin samun nasara yayin da aka fifita rabon gaggawa na duniya a kan kamanta umarnin Allah.**

**4 - Falalar saukar nutsuwa, nutsuwar Manzon Allah (S.A.W) nutsuwa ce ga musulman da suke tare da shi, da tabbacin samun nasara. Nutsuwar muminai kuwa nutsuwa ce ta tabbata, da jarunta bayan raki da jin tsoro.**

ثُمَّ يَتُوبُ ٱللَّهُ مِنۢ بَعۡدِ ذَٰلِكَ عَلَىٰ مَن يَشَآءُۗ وَٱللَّهُ
غَفُورٞ رَّحِيمٞ ٢٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُوٓاْ إِنَّمَا ٱلۡمُشۡرِكُونَ
نَجَسٞ فَلَا يَقۡرَبُواْ ٱلۡمَسۡجِدَ ٱلۡحَرَامَ بَعۡدَ عَامِهِمۡ هَٰذَاۚ
وَإِنۡ خِفۡتُمۡ عَيۡلَةٗ فَسَوۡفَ يُغۡنِيكُمُ ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦٓ
إِن شَآءَۚ إِنَّ ٱللَّهَ عَلِيمٌ حَكِيمٞ ٢٨ قَٰتِلُواْ ٱلَّذِينَ
لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَلَا بِٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ وَلَا يُحَرِّمُونَ
مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ وَلَا يَدِينُونَ دِينَ ٱلۡحَقِّ مِنَ
ٱلَّذِينَ أُوتُواْ ٱلۡكِتَٰبَ حَتَّىٰ يُعۡطُواْ ٱلۡجِزۡيَةَ عَن يَدٖ
وَهُمۡ صَٰغِرُونَ ٢٩ وَقَالَتِ ٱلۡيَهُودُ عُزَيۡرٌ ٱبۡنُ ٱللَّهِ
وَقَالَتِ ٱلنَّصَٰرَى ٱلۡمَسِيحُ ٱبۡنُ ٱللَّهِۖ ذَٰلِكَ قَوۡلُهُم
بِأَفۡوَٰهِهِمۡۖ يُضَٰهِـُٔونَ قَوۡلَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ مِن قَبۡلُۚ
قَٰتَلَهُمُ ٱللَّهُۖ أَنَّىٰ يُؤۡفَكُونَ ٣٠ ٱتَّخَذُوٓاْ أَحۡبَارَهُمۡ
وَرُهۡبَٰنَهُمۡ أَرۡبَابٗا مِّن دُونِ ٱللَّهِ وَٱلۡمَسِيحَ ٱبۡنَ
مَرۡيَمَ وَمَآ أُمِرُوٓاْ إِلَّا لِيَعۡبُدُوٓاْ إِلَٰهٗا وَٰحِدٗاۖ
لَّآ إِلَٰهَ إِلَّا هُوَۚ سُبۡحَٰنَهُۥ عَمَّا يُشۡرِكُونَ ٣١



**(27) Sannan wanda ya tuba daga kafircinsa da vatansa bayan wannan azabtarwar, to haqiqa Allah zai yafe masa, ya karvi tubansa. Allah mai yawan gafara ne ga bayinsa, mai jinqansu ne, ta yadda yake karvar tubansu bayan kafirci da aikata ayyukan savo.**

**(28) Ya waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, suka bi abin da ya shar'anta musu, ku sani mushirikai najasa ne, saboda abin da suke kai na kafirci da zalunci da munanan halaye da al'adu marasa kyau, don haka kada su qara shiga haramin Makkah – wanda daga cikinsa akwai masallacin harami – ko da kuwa sun kasance alhazai ko masu yin umara, daga wannan shekara ta tara bayan hijira. Idan kuna jin tsoron talauci – ya ku muminai – saboda yankewar abin da suke kawo muku na abinci da kayan kasuwanci daban-daban, to ku sani haqiqa Allah zai isar muku da falalarsa, in ya ga dama. Haqiqa Allah masani ne da halin da kuke ciki, kuma mai hikima ne cikin abin da yake tsara muku.**

**(29) Yaku muminai ku yaqi kafiran da ba su yi imani da Allah shi ne abin bauta ba, bai da abokin tarayya, ba su yi imani da ranar alqiyama ba, ba sa nisantar abin da Allah da Manzonsa suka haramta shi, na mushe da naman Alade, da giya, da riba, kuma ba sa sunkuya wa zuwa ga abin da Allah ya shar'anta, daga cikin Yahudu da Nasara, har sai sun bada jizya da hannayensu, suna maqasqanta wanda aka rinjaya.**

**(30) Yahudawa da Nasara su duka mushirikai ne. Yahudawa sun yi shirka da Allah yayin da suka yi da'awar cewa Uzairu xan Allah ne, su kuma Nasara sun yi shirka da Allah yayin da suka yi da'awar Almasihu Isa xan Allah ne. Wannan magana ce da suka qirqira suka faxe ta da bakinsu, ba tare da wata hujja ko dalili ba, don haka sun yi kama da waxanda suka gabace su daga mushirikai a cikin wannan abin da suka faxa, waxanda suka ce: "Mala'iku 'ya'yan Allah ne mata – Allah ya xaukaka daga abin da suke faxa, xaukaka mai girma –" Allah ya halakar da su, ta yaya ake kawar da su daga gaskiya bayyananniya zuwa ga varna?".**

**(31) Yahudawa sun mayar da malamansu ababen bautawarsu, haka ma Nasara su ma sun mayar da masu ibadarsu, ababen bauta koma bayan Allah, suna halatta musu abin da Allah ya haramta musu, kuma suna haramta musu abin da Allah ya halatta musu. Nasara sun sanya Almasihu Isa xan Maryam abin bauta tare da Allah, alhali Allah bai umarci malaman Yahudawa da masu ibadar Nasara da Uzairu da Isa xan Maryam da komai ba, sai dai su bauta masa shi kaxai, kada su yi shirka da shi da komai, Shi kaxai - tsarki ya tabbata a gare shi – shi ne abin bauta wa shi kaxai, babu wani abin bauta wa da gaskiya, wanda ba shi ba, tsarki ya tabbata a gare shi, bai da abokin tarayya, kamar yadda waxannan mushirikai da waninsu suke faxa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - A cikin ayoyin akwai dalili akan halaccin rataya zuciya da sabubban arziki, hakan kuma baya kore dogaro ga Allah.**

**2 - A cikin ayoyin akwai dalilin da yake nuna ba dagewa ba ce take kawo arziki, falalar Allah Maxaukakin Sarki ce kawai, Shi yake raba shi.**

**3 - Jizya xaya ce daga cikin zavi guda uku da musulunci yake bijirarwa ga maqiya, da manufar dukkan lamari gaba xaya ya zama na musulunci, kuma a cire qarfin kafirai.**

**4 - Yahudawa suna xauke da muni da sharrin da suka kai su zuwa ga yi wa Allah rashin kunya, suka tauye girmansa, tsarki ya tabbata a gare shi.**

يُرِيدُونَ أَن يُطْفِـُٔواْ نُورَ ٱللَّهِ بِأَفْوَٰهِهِمْ وَيَأْبَى ٱللَّهُ إِلَّآ أَن
يُتِمَّ نُورَهُۥ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْكَٰفِرُونَ ٣٢ هُوَ ٱلَّذِىٓ أَرْسَلَ
رَسُولَهُۥ بِٱلْهُدَىٰ وَدِينِ ٱلْحَقِّ لِيُظْهِرَهُۥ عَلَى ٱلدِّينِ
كُلِّهِۦ وَلَوْ كَرِهَ ٱلْمُشْرِكُونَ ٣٣ ۞ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ الحزب ٢٠
ءَامَنُوٓاْ إِنَّ كَثِيرًا مِّنَ ٱلْأَحْبَارِ وَٱلرُّهْبَانِ لَيَأْكُلُونَ
أَمْوَٰلَ ٱلنَّاسِ بِٱلْبَٰطِلِ وَيَصُدُّونَ عَن سَبِيلِ ٱللَّهِ ۗ وَٱلَّذِينَ
يَكْنِزُونَ ٱلذَّهَبَ وَٱلْفِضَّةَ وَلَا يُنفِقُونَهَا فِى
سَبِيلِ ٱللَّهِ فَبَشِّرْهُم بِعَذَابٍ أَلِيمٍ ٣٤ يَوْمَ يُحْمَىٰ عَلَيْهَا
فِى نَارِ جَهَنَّمَ فَتُكْوَىٰ بِهَا جِبَاهُهُمْ وَجُنُوبُهُمْ
وَظُهُورُهُمْ ۖ هَٰذَا مَا كَنَزْتُمْ لِأَنفُسِكُمْ فَذُوقُواْ مَا كُنتُمْ
تَكْنِزُونَ ٣٥ إِنَّ عِدَّةَ ٱلشُّهُورِ عِندَ ٱللَّهِ ٱثْنَا عَشَرَ
شَهْرًا فِى كِتَٰبِ ٱللَّهِ يَوْمَ خَلَقَ ٱلسَّمَٰوَٰتِ وَٱلْأَرْضَ مِنْهَآ
أَرْبَعَةٌ حُرُمٌ ۚ ذَٰلِكَ ٱلدِّينُ ٱلْقَيِّمُ ۚ فَلَا تَظْلِمُواْ فِيهِنَّ
أَنفُسَكُمْ ۚ وَقَٰتِلُواْ ٱلْمُشْرِكِينَ كَآفَّةً كَمَا
يُقَٰتِلُونَكُمْ كَآفَّةً ۚ وَٱعْلَمُوٓاْ أَنَّ ٱللَّهَ مَعَ ٱلْمُتَّقِينَ ٣٦



**(32) Waxannan kafirai da ire-irensu waxanda suke kan wani addini na kafirci suna nufin warware musulunci su vata shi, ta haryar qirqiro qarya, da qaryatawarsu ga abin da Manzon Allah Muhammad (S.A.W) ya zo da shi, su vata abin da yake cikinsa na hujjoji bayyanannu da dalilai a kan kaxaitakar Allah da nuna abin da Manzonsa ya zo da shi gaskiya ne, amma Allah ya qi sai ya cika addininsa, ya bayyana shi, ya xaukaka shi a kan waninsa, ko da kafirai sun qi, ba sa son cika addininsa da xaukaka shi, amma Allah zai cika shi, ya xaukaka shi. Idan Allah ya yi nufin wani lamari ya tabbata sai ya lalata abin da waninsa ya nufata.**

**(33) Allah Maxaukakin Sarki shi ne wanda ya aiko da Manzonsa Muhammad (S.A.W) da Alqur'ani, wanda shiriya ne ga mutane. Kuma ya aiko shi da addinin musulunci, don ya xaukaka shi da abin da yake cikinsa na hujjoji da dalilai da hukunce-hukunce a kan sauran addinai, ko da mushirikai sun qi hakan.**

**(34) Ya waxanda suka yi imani, suka yi aiki da abin da Allah ya shar'anta musu, ku sani da yawa daga cikin malaman Yahudawa, da da yawa daga masu ibada a cikin Nasara, suna karvar dukiyar mutane ba da haqqi na shari'a ba, suna karva da sunan cin hanci da waninsa, kuma suna hana mutane shiga cikin addinin Allah. Waxanda suke tara zinare da azurfa, kuma ba sa bada abin da ya wajaba a kansu na zakka, to ya kai wannan manzo ka basu labari da abin da zai baqanta musu rai ranar alqiyama na azaba mai raxaxi.**

**(35) Ranar alqiyama za a kunna wa abin da suka tara wuta, idan ta yi zafi, sai a xora ta a kan goshinsu da gefensu da bayansu, a ce musu cikin wulaqantarwa: "Wannan ita ce dukiyarku wadda kuka tara, ba ku ba da haqqoqin da suka wajaba a kanku ba, ku xanxani azabar abin da kuka kasance kuna tarawa, ba tare da kun ba da zakkarsa ba.**

**(36) Haqiqa adadin watannin shekara a hukuncin Allah da qaddarawarsa wata goma sha biyu ne, daga cikin abin da Allah ya tabbatar da shi a Lauhul Mahfuz, tun farkon halittar sammai da qassai. Daga cikin waxannan watanni sha biyu akwai guda huxu da Allah ya haramta yaqi a cikinsu, uku a jere suke su ne (Zul-qa'ada, Zul-hijjah, Almuharram) guda xaya kuma a ware yake, shi ne (Rajab). Waxannan adadi da aka ambata na watannin shekara, da haramta zalunci a cikin guda huxu, shi ne addini madaidaici, don haka ka da ku zalunci kawunanku a cikin waxannan watanni masu alfarma, ta hanyar yin yaqi a cikinsu, da keta alfarmarsu. Ku yaqi mushirikai gaba xaya, kamar yadda su ma suke yaqarku gaba xaya. Ku sani haqiqa Allah yana tare da waxanda suke tsoronsa, ta hanyar kamanta abin da ya umarta, da nisantar abin da ya hana, yana tare da su da ba da nasara da tabbatarwa. Duk wanda Allah yake tare da shi, ba wanda zai rinjaye shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Addinin Allah a bayyane yake, kuma mai cin nasara ne, duk da irin abin da maqiyansa suke yi don cutar da shi, saboda hassadarsu.**

**2 - Haramcin cin dukiyar mutane da varna, da kange mutane daga tafarkin Allah Maxaukakin Sarki.**

**3 - Haramcin taskace dukiya ba tare da ciyarwa a kan tafarkin Allah ba.**

**4 - Kwaxaitarwa a kan tsoron Allah a fili da voye, musamman ma a wurin yaqar kafirai, saboda mumini yana tsoron Allah a kowane hali.**

إِنَّمَا ٱلنَّسِىٓءُ زِيَادَةٞ فِي ٱلۡكُفۡرِۖ يُضَلُّ بِهِ ٱلَّذِينَ
كَفَرُواْ يُحِلُّونَهُۥ عَامٗا وَيُحَرِّمُونَهُۥ عَامٗا لِّيُوَاطِـُٔواْ
عِدَّةَ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُ فَيُحِلُّواْ مَا حَرَّمَ ٱللَّهُۚ زُيِّنَ لَهُمۡ
سُوٓءُ أَعۡمَٰلِهِمۡۗ وَٱللَّهُ لَا يَهۡدِي ٱلۡقَوۡمَ ٱلۡكَٰفِرِينَ
٣٧ يَٰٓأَيُّهَا ٱلَّذِينَ ءَامَنُواْ مَا لَكُمۡ إِذَا قِيلَ لَكُمُ
ٱنفِرُواْ فِي سَبِيلِ ٱللَّهِ ٱثَّاقَلۡتُمۡ إِلَى ٱلۡأَرۡضِۚ أَرَضِيتُم
بِٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا مِنَ ٱلۡأٓخِرَةِۚ فَمَا مَتَٰعُ ٱلۡحَيَوٰةِ
ٱلدُّنۡيَا فِي ٱلۡأٓخِرَةِ إِلَّا قَلِيلٌ ٣٨ إِلَّا تَنفِرُواْ يُعَذِّبۡكُمۡ
عَذَابًا أَلِيمٗا وَيَسۡتَبۡدِلۡ قَوۡمًا غَيۡرَكُمۡ وَلَا تَضُرُّوهُ
شَيۡـٔٗاۗ وَٱللَّهُ عَلَىٰ كُلِّ شَيۡءٖ قَدِيرٌ ٣٩ إِلَّا تَنصُرُوهُ
فَقَدۡ نَصَرَهُ ٱللَّهُ إِذۡ أَخۡرَجَهُ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ثَانِيَ ٱثۡنَيۡنِ
إِذۡ هُمَا فِي ٱلۡغَارِ إِذۡ يَقُولُ لِصَٰحِبِهِۦ لَا تَحۡزَنۡ إِنَّ ٱللَّهَ
مَعَنَاۖ فَأَنزَلَ ٱللَّهُ سَكِينَتَهُۥ عَلَيۡهِ وَأَيَّدَهُۥ بِجُنُودٖ
لَّمۡ تَرَوۡهَا وَجَعَلَ كَلِمَةَ ٱلَّذِينَ كَفَرُواْ ٱلسُّفۡلَىٰۗ
وَكَلِمَةُ ٱللَّهِ هِيَ ٱلۡعُلۡيَاۗ وَٱللَّهُ عَزِيزٌ حَكِيمٌ ٤٠



(37) Haqiqa jinkirta alfarmar watan da aka haramta yaqi a cikinsa, zuwa wani watan da ba a haramta ba, da sanya watan da aka haramta a wurin wanda ba a haramta ba, kamar yadda larabawan jahiliyya suke aikatawa, qarin kafirci ne a kan kafirce wa Allah, don sun kafirce wa hukuncin Allah a cikin watanni masu alfarma, kuma Shaixan ne yake vatar da waxanda suke kafirce wa Allah, ta yadda ya sunnata musu wannan mummunar sunnah, suna halatta wata mai alfarma a shekara, su canza shi da wani daga cikin watannin da aka halatta, a wata shekarar kuma sai su bar shi a kan haramcinsa, don ya dace da adadin watannin da Allah ya haramta, duk da sun savawa haqiqanin watannin, don ba sa halatta wani wata, face sai sun sanya wani a wurinsa, da haka sai su halatta abin da Allah ya haramta na watanni, su savawa hikimar Allah. Shaixan ya qawata musu munanan ayyukansu, har suka aikata su, daga ciki akwai abin da suka qirqiro na jinkirtawa. Allah ba ya datar da kafirai masu dagewa a kan kafircinsu zuwa ga shiriya.
(38) Ya waxanda suka yi imani da Allah da Manzonsa, suka yi aiki da abin da Allah ya shar'anta musu, meye ya same ku idan in kiraku zuwa ga jihadi a kan tafarkin Allah, don yaqar maqiyanku, sai ku yi jinkiri, ku karkata zuwa ga zama a gidajenku? Kun yarda da daxin duniya mai gushewa, da kayan daxinta masu yankewa, a maimakon ni'imar lahira mai dauwama, wadda Allah ya tanadar wa masu jihadi a kan tafarkinsa?!. To jin daxin duniya a kan na lahira
ba komai ba ne, face wulaqantacce, kuma ta yaya mai hankali zai zavi mai qare wa a kan wanda yake ba ya qarewa,
ya zavi wulaqantacce a kan mai girma?!. (39) Yaku muminai in baku fita zuwa jihadi a kan tafarkin Allah don
yaqar abokan gabarku ba, Allah zai yi muku uquba ta qasqantawa da waninta, ya canzaku da wasu mutane masu
bin Allah, waxanda idan an nemi su fita jihadi, za su fita. Ba kuma zaku cutar da Allah da komai ba, idan kun sava
masa, ya wadatu daga gare ku, ku kuma mabuqata ne gare shi. Allah mai iko ne a kan dukkan komai, babu abin
da yake gagararsa, yana da iko a kan taimakon addininsa da Annabinsa, ba tare da ku ba.

(40) Yaku muminai idan baku taimaki Manzon Allah ba (S.A.W) kuka amsa kiransa zuwa ga jihadi a kan tafarkin Allah ba, to haqiqa Allah ya taimake shi, ba tare da kuna tare da shi ba, yayin da mushirikai suka fitar da shi (S.A.W) da Abubakar (R.A), ba wani na uku a tare da su, yayin da suka kasance a cikin kogon da ake kira da Garii Saurin, saboda voye wa kafiran da suke nemansu, a lokacin da Manzon Allah (S.A.W) yake cewa abokinsa Abubakar siddiq, lokacin da ya ji tsoron ka da mushirikai su riski Manzon Allah (S.A.W) ya ce da shi: "Kada ka yi baqin ciki, haqiqa Allah yana tare da mu, da qarfafawarsa da nasararsa", sai Allah ya saukar da nutsuwa a zuciyar Manzon Allah, ya saukar masa da rundunar da ba kwa ganinsu, su ne Mala'iku, suna qarfafa shi, ya sanya kalmar mushirikai a qasa, kalmar Allah a sama, ya xaukaka musulunci. Allah Mabuwayi ne a zatinsa da qarfinsa, da mulkinsa, babu wanda yake rinjayarsa, mai hikima ne a cikin tsarinsa da qaddarawarsa da shari'arsa.

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** 1 - Ci gaba da aikata munanan al'adun da suka savawa shari'a, ba tare da hani ba, yana sa muninsu ya gushe daga zukata, wataqila ma a riqa zatonsu al'adu ne masu kyau. 2 - Rashin fita yaqi a lokacin da aka nemi fita, yana daga cikin manya-manyan zunubai, waxanda suke wajabta uquba mai tsanani, saboda tsananin cutarwar dake ciki. 3 - Falalar nutsuwa, kuma tana cikin cikar ni'imar Allah ga bawa, a yayin tsanani da jin tsoron da zukata suke karkacewa a lokacinsu. Kuma nutsuwa tana samuwa ne gwargwadon yadda bawa ya san Ubangijinsa, da yardarsa da alqawarinsa na gaskiya, sannan kuma gwargwadon imaninsa da jarumtarsa. 4 - Baqin ciki da damuwa za su iya bijirowa bayin Allah siddiqai, musamman ma yayin jin tsoron kuvucewar wata maslaha gamammiya.

ٱنفِرُواْ خِفَافٗا وَثِقَالٗا وَجَٰهِدُواْ بِأَمۡوَٰلِكُمۡ وَأَنفُسِكُمۡ
فِي سَبِيلِ ٱللَّهِۚ ذَٰلِكُمۡ خَيۡرٞ لَّكُمۡ إِن كُنتُمۡ تَعۡلَمُونَ
﴿٤١﴾ لَوۡ كَانَ عَرَضٗا قَرِيبٗا وَسَفَرٗا قَاصِدٗا لَّٱتَّبَعُوكَ
وَلَٰكِنۢ بَعُدَتۡ عَلَيۡهِمُ ٱلشُّقَّةُۚ وَسَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ
لَوِ ٱسۡتَطَعۡنَا لَخَرَجۡنَا مَعَكُمۡ يُهۡلِكُونَ أَنفُسَهُمۡ وَٱللَّهُ
يَعۡلَمُ إِنَّهُمۡ لَكَٰذِبُونَ ﴿٤٢﴾ عَفَا ٱللَّهُ عَنكَ لِمَ أَذِنتَ لَهُمۡ
حَتَّىٰ يَتَبَيَّنَ لَكَ ٱلَّذِينَ صَدَقُواْ وَتَعۡلَمَ ٱلۡكَٰذِبِينَ
﴿٤٣﴾ لَا يَسۡتَـٔۡذِنُكَ ٱلَّذِينَ يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ أَن
يُجَٰهِدُواْ بِأَمۡوَٰلِهِمۡ وَأَنفُسِهِمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِٱلۡمُتَّقِينَ ﴿٤٤﴾
إِنَّمَا يَسۡتَـٔۡذِنُكَ ٱلَّذِينَ لَا يُؤۡمِنُونَ بِٱللَّهِ وَٱلۡيَوۡمِ ٱلۡأٓخِرِ
وَٱرۡتَابَتۡ قُلُوبُهُمۡ فَهُمۡ فِي رَيۡبِهِمۡ يَتَرَدَّدُونَ ﴿٤٥﴾ ۞ وَلَوۡ
أَرَادُواْ ٱلۡخُرُوجَ لَأَعَدُّواْ لَهُۥ عُدَّةٗ وَلَٰكِن كَرِهَ ٱللَّهُ ٱنۢبِعَاثَهُمۡ
فَثَبَّطَهُمۡ وَقِيلَ ٱقۡعُدُواْ مَعَ ٱلۡقَٰعِدِينَ ﴿٤٦﴾ لَوۡ خَرَجُواْ فِيكُم
مَّا زَادُوكُمۡ إِلَّا خَبَالٗا وَلَأَوۡضَعُواْ خِلَٰلَكُمۡ يَبۡغُونَكُمُ
ٱلۡفِتۡنَةَ وَفِيكُمۡ سَمَّٰعُونَ لَهُمۡۗ وَٱللَّهُ عَلِيمُۢ بِٱلظَّٰلِمِينَ ﴿٤٧﴾

الحِزْبُ ٢٠



**(41) Yaku muminai ku yi tafiya don yin jihadi a kan tafarkin Allah, a cikin qunci da yalwa, kuna matasa ko tsofaffi. Ku yi jihadi da dukiyoyinku da rayukanku. Saboda fita don yin jihadi da dukiya da rayuka ya fi amfani a duniya fiye da zama da dogara akan kuvutar dukiya da rayuka, in kun san haka, to ku yi qoqarin aikatawa.**

**(42) Da wata ganima ce mai sauqi, ko wata tafiyar da babu wahala a cikinta, kake kiran waxannan da suka nemi uzurinka daga cikin munafukai, da sun bi ka, sai dai da yake tafiyar da kake kiransu zuwa gare ta don yaqar abokan gaba tana da nisa, don haka suka qi zuwa, waxannan masu neman uzurin daga cikin munafukai za su rantse maka da Allah yayin da ka dawo, su ce,: "Da zamu iya fita zuwa jihadi tare da ku, da mun fita". Suna halakar da kawunansu, ta hanyar bijirar da su ga uqubar Allah, saboda qin zuwansu yaqi da kuma waxannan rantse-rantsen qaryar. Allah ya san qarya suke a da'awarsu, da rantse-rantsensu.**

**(43) Allah ya yi maka afuwa – ya kai wannan Manzo – a kan ijtihadinka da ka yi na basu izinin qin zuwa yaqi, don me ka yi musu izini? Da ka jinkirta har sai ka gane masu gaskiya a cikin uzurin da suka gabatar, da waxanda suka yi qarya, sai ka yi wa masu gaskiya izini daga cikinsu, ka qyale maqaryata.**

**(44) Ba aikin waxanda suka yi imani da Allah da ranar alqiyama, imani na gaskiya bane, su nemi izinin qin zuwa yaqi da dukiyoyinsu da rayukansu a kan tafarkin Allah daga wajenka ba – ya kai wannan Manzo -. Aikinsu shi ne su fita duk lokacin da aka ce a fita, su yi jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu. Allah yana sane da masu tsoronsa daga cikin bayinsa, waxanda basa neman izinin qin fita, sai dai in da uzurin da zai hana su fita tare da kai.**

**(45) Ya kai wannan Manzo waxanda suke neman izini na qin zuwa jihadi a kan tafarkin Allah su ne munafukai, waxanda ba sa imani da Allah, basa imani da ranar lahira, kuma shakka a cikin addinin Allah ta kama zuciyarsu, don haka suna cikin kai-kawo a cikin shakkarsu, suna ruxaxxu basa gane gaskiya.**

**(46) Da masu gaskiya ne a cikin da'awarsu cewa suna son fita tare da kai don yin jihadi a kan tafarkin Allah, da sun shirya masa, ta hanyar tanadi, sai dai Allah ya qi fitar su tare da kai, sai fitar ta yi musu nauyi, har suka zavi zama a gidajensu.**

**Yayin da rashin fitar waxannan yake baqanta wa muminai rai, sai Allah ya kwantar musu da hankali, ya nuna musu cutar fitarsu ta fi ta zamansu a gida yawa, ya ce:**

**(47) Yana daga cikin alheri kada waxannan munafukai su fita tare da ku, domin in sun fita tare da ku, ba abin da za su qara muku sai varna, saboda abin da za su yi na qasqantawa da jefa shubuha, kuma da sun yi gaggawar yaxa gulma a cikinku, don su raba kanku, ga shi a cikinku – Ku muminai – akwai wanda yake sauraran abin da suke yaxawa na qarya, ya karva, ya yaxa shi, sai savani ya faru a tsakaninku. Allah yana sane da azzalumai daga cikin munafukai waxanda suke jefa makirci da shakka a tsakanin muminai.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin yin jihadi da rai da dukiya a duk lokacin da buqatar hakan ta taso.**

**2 - Rantse-rantsen qarya suna jawo halaka.**

**3 - Wajabcin kula da rashin gaggawa, da wajabcin tabbatarwa da nutsuwa, da barin ruxuwa da zahirin abubuwa, da kai matuqa wajen tacewa da bi-sannu-sannu.**

**4 - Yana daga cikin kulawar Allah ga muminai daskarar da munafukai da hana su fita tare da bayinsa muminai, don jin qai ga muminai da tausaya musu, kada abin da bai zai amfane su ba, sai dai ya cutar da su, ya shige su.**

لَقَدِ ٱبۡتَغَوُاْ ٱلۡفِتۡنَةَ مِن قَبۡلُ وَقَلَّبُواْ لَكَ ٱلۡأُمُورَ حَتَّىٰ
جَآءَ ٱلۡحَقُّ وَظَهَرَ أَمۡرُ ٱللَّهِ وَهُمۡ كَٰرِهُونَ ٤٨ وَمِنۡهُم
مَّن يَقُولُ ٱئۡذَن لِّي وَلَا تَفۡتِنِّيٓۚ أَلَا فِي ٱلۡفِتۡنَةِ سَقَطُواْۗ وَإِنَّ
جَهَنَّمَ لَمُحِيطَةُۢ بِٱلۡكَٰفِرِينَ ٤٩ إِن تُصِبۡكَ
حَسَنَةٞ تَسُؤۡهُمۡۖ وَإِن تُصِبۡكَ مُصِيبَةٞ يَقُولُواْ قَدۡ
أَخَذۡنَآ أَمۡرَنَا مِن قَبۡلُ وَيَتَوَلَّواْ وَّهُمۡ فَرِحُونَ ٥٠ قُل
لَّن يُصِيبَنَآ إِلَّا مَا كَتَبَ ٱللَّهُ لَنَا هُوَ مَوۡلَىٰنَاۚ وَعَلَى
ٱللَّهِ فَلۡيَتَوَكَّلِ ٱلۡمُؤۡمِنُونَ ٥١ قُلۡ هَلۡ تَرَبَّصُونَ بِنَآ إِلَّآ
إِحۡدَى ٱلۡحُسۡنَيَيۡنِۖ وَنَحۡنُ نَتَرَبَّصُ بِكُمۡ أَن يُصِيبَكُمُ ٱللَّهُ
بِعَذَابٖ مِّنۡ عِندِهِۦٓ أَوۡ بِأَيۡدِينَاۖ فَتَرَبَّصُوٓاْ إِنَّا مَعَكُم
مُّتَرَبِّصُونَ ٥٢ قُلۡ أَنفِقُواْ طَوۡعًا أَوۡ كَرۡهٗا لَّن يُتَقَبَّلَ
مِنكُمۡ إِنَّكُمۡ كُنتُمۡ قَوۡمٗا فَٰسِقِينَ ٥٣ وَمَا
مَنَعَهُمۡ أَن تُقۡبَلَ مِنۡهُمۡ نَفَقَٰتُهُمۡ إِلَّآ أَنَّهُمۡ كَفَرُواْ
بِٱللَّهِ وَبِرَسُولِهِۦ وَلَا يَأۡتُونَ ٱلصَّلَوٰةَ إِلَّا وَهُمۡ
كُسَالَىٰ وَلَا يُنفِقُونَ إِلَّا وَهُمۡ كَٰرِهُونَ ٥٤



**(48) Waxannan munafukai sun yi kwaxayin varna da raba kan muminai, da wargaza su kafin fita yaqin Tabuka, sun yi maka abubuwa kala-kala, da dabara daban-daban – ya kai wannan Manzo – don su samu yin tasiri a kan azamarka ta fita jihadi, har sai da lamarin Allah ya zo da qarfafa ka, Allah ya qarfafa addininsa, ya rinjayi maqiyansa, amma su basu so hakan ba, saboda suna kwaxayin varna ta samu nasara a kan gaskiya.**

**(49) Daga cikin munafukai akwai wanda yake bada uzuri na qarya, ya ce: “Ya Manzon Allah, ka yi min izinin kada in je jihadi, kada ka takura min fita tare da kai, don kada in gamu da zunubi, shi ne na fitinar matan abokan gaba – wato Rumawa – idan na gansu”. Ku saurara! Haqiqa sun faxa fitinar da tafi wadda suka raya girma, ita ce fitinar munafunci, da qin zuwa jihadi. Kuma haqiqa Jahannama mai kewaye kafirai ce ranar alqiyama, babu wanda zai kubce mata, kuma ba za su samu damar gudu daga gare ta ba.**

**(50) Ya Manzon Allah idan wata ni’ima ta same ka daga Allah, ta farin cikin samun nasara, ko ganima, ba sa son hakan, sai su yi baqin ciki, amma in wata musifa mai tsanani ko samun nasarar abokan gaba a kanka ya same ka, sai waxannan munafukai su ce: “Mun riga mun xau mataki ga kawunanmu, mun yi riqo da daidai yayin da bamu fita yaqi, kamar yadda muminai suka fita ba, har abin da ya same su, na kisa da kamu ya same su”, sai waxannan munafukai su juya zuwa ga iyalansu suna farin cikin kuvuta da suka yi.**

**(51) Ya kai wannan Manzo ka cewa waxannan munafukai: “Ba abin da zai same mu, sai abin da Allah ya rubuta mana, Shi ne shugabanmu, makomarmu, wadda muke komawa gare ta, mun dogara a gare shi cikin al’amuranmu, kuma gare shi, shi kaxai muminai suke mayar da al’amuransu, ya isar musu, madallah da abin dogaro.**

**(52) Ya kai wannan Manzo ka ce musu: Ba abin da kuke jira a kanmu, sai nasara ko shahada!. Mu kuwa muna jiran Ubangijinku ya saukar muku da azaba daga wajensa, ya halaka ku da ita, ko ya azabtar da ku, da hannuwanmu, ta hanyar kashe ku, da kama ku, idan ya yi mana izinin mu yaqe ku, ku jira qarshenmu, muma zamu jira qarshenku.**

**(53) Ya kai wannan Manzo ka ce da su: “Ku ciyar da abin da zaku ciyar na dukiyoyinku, kuna so, ko ba kwa so, ba za a karvi abin da kuka ciyar ba, saboda kafircinku da fitar ku daga xa’ar Allah”.**

**(54) Ba abin da ya hana a karvi ciyarwarsu sai abubuwa guda uku: kafircinsu ga Allah da Manzonsa, da kasalarsu da nauyinsu idan za su yi sallah, sannan ba sa ciyar da dukiyar da son ransu, suna ciyar da ita ne a kan dole, saboda basa fatan samun ladan sallolinsu, ko ciyarwar su.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Al’adar munafukai yin aiki don cutar da musulmai ta hanyar makirci da bin diddigi.**

**2 - Qin zuwa jihadi varna ce babba, kuma fitina ce mai girma tabbatacciya, kuma savon Allah ne da Manzonsa.**

**3 - A cikin ayoyin akwai koyawa musulmi kada su yi baqin ciki da abin da ya same su, saboda kada su yi rauni, qarfinsu ya tafi, kuma su yarda da abin da Allah ya qaddara musu, su yi fatan samun yardar Ubangijinsu, saboda sun yi imanin Allah yana nufin taimakon addininsa.**

**4 - Yana daga alamar raunin imani da qarancin tsoron Allah, yin kasala a wajen sallah da ciyarwa ba tare da yarda da fatan samun ladan Allah ba.**

فَلَا تُعۡجِبۡكَ أَمۡوَٰلُهُمۡ وَلَآ أَوۡلَٰدُهُمۡۚ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ لِيُعَذِّبَهُم
بِهَا فِي ٱلۡحَيَوٰةِ ٱلدُّنۡيَا وَتَزۡهَقَ أَنفُسُهُمۡ وَهُمۡ كَٰفِرُونَ
(٥٥) وَيَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ إِنَّهُمۡ لَمِنكُمۡ وَمَا هُم مِّنكُمۡ وَلَٰكِنَّهُمۡ
قَوۡمٞ يَفۡرَقُونَ (٥٦) لَوۡ يَجِدُونَ مَلۡجَـًٔا أَوۡ مَغَٰرَٰتٍ أَوۡ مُدَّخَلٗا
لَّوَلَّوۡاْ إِلَيۡهِ وَهُمۡ يَجۡمَحُونَ (٥٧) وَمِنۡهُم مَّن يَلۡمِزُكَ فِي
ٱلصَّدَقَٰتِ فَإِنۡ أُعۡطُواْ مِنۡهَا رَضُواْ وَإِن لَّمۡ يُعۡطَوۡاْ مِنۡهَآ إِذَا
هُمۡ يَسۡخَطُونَ (٥٨) وَلَوۡ أَنَّهُمۡ رَضُواْ مَآ ءَاتَىٰهُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
وَقَالُواْ حَسۡبُنَا ٱللَّهُ سَيُؤۡتِينَا ٱللَّهُ مِن فَضۡلِهِۦ وَرَسُولُهُۥٓ
إِنَّآ إِلَى ٱللَّهِ رَٰغِبُونَ (٥٩) ۞ إِنَّمَا ٱلصَّدَقَٰتُ لِلۡفُقَرَآءِ وَٱلۡمَسَٰكِينِ نصف الحزب
وَٱلۡعَٰمِلِينَ عَلَيۡهَا وَٱلۡمُؤَلَّفَةِ قُلُوبُهُمۡ وَفِي ٱلرِّقَابِ
وَٱلۡغَٰرِمِينَ وَفِي سَبِيلِ ٱللَّهِ وَٱبۡنِ ٱلسَّبِيلِۖ فَرِيضَةٗ
مِّنَ ٱللَّهِۗ وَٱللَّهُ عَلِيمٌ حَكِيمٞ (٦٠) وَمِنۡهُمُ ٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ
ٱلنَّبِيَّ وَيَقُولُونَ هُوَ أُذُنٞۚ قُلۡ أُذُنُ خَيۡرٖ لَّكُمۡ يُؤۡمِنُ
بِٱللَّهِ وَيُؤۡمِنُ لِلۡمُؤۡمِنِينَ وَرَحۡمَةٞ لِّلَّذِينَ ءَامَنُواْ
مِنكُمۡۚ وَٱلَّذِينَ يُؤۡذُونَ رَسُولَ ٱللَّهِ لَهُمۡ عَذَابٌ أَلِيمٞ (٦١)



**(55) Ya kai wannan Manzo kada dukiyar munafukai da ‘ya’yansu su qayatar da kai, kada ka ga kyansu, makomar dukiyoyinsu da ‘ya’yansu mummuna ce, Allah zai sanya su azaba a kansu, ta hanyar wahala wajen tara ta, da kuma abin da zai saukar musu na musifa, har zuwa fitar rayukansu, suna kafirai, ya azabta su da dauwama a can qasan wuta.**

**(56) Munafukai suna muku rantsuwa – Ku muminai – suna qaryar cewa: “Su suna cikinku, alhali basa cikinku a voye, duk da sun bayyana suna tare da ku, sai dai su mutane ne da suke jin tsoron abin da ya faru ga mushirikai na kisa da kamu kada ya faru a kansu, don haka sai su bayyana musulunci don munafunci.**

**(57) Da waxannan munafukai za su samu wata mafaka ta wani gini, da zasu kare rayukansu a cikinta, ko su samu wani kogo a cikin duwatsu, da za su voye a cikinsa, ko su samu wani rami, da za su shiga su fake a cikinsa, da sun shiga da gaggawa cikin farin ciki da annashuwa.**

**(58) Daga cikin munafukai akwai waxanda suke aibata ka – Ya kai wannan Manzo – a kan raba sadaka, a yayin da ba su samu abin da suke so ba, idan ka basu daga cikinta, sai su yarda da kai, idan baka ba su abin da suke nema ba, sai su nuna damuwa. (59) Da a ce waxannan munafukai, waxanda suke aibata ka a kan rabon sadaka, sun yarda da abin da Allah ya farlanta a basu, sun yarda da abin da ka basu daga cikinta, kuma suka ce: “Allah ya isar mana, zai ba mu abin da ya ga dama daga falalarsa, Manzon Allah zai ba mu daga abin da Allah ya ba shi, ga Allah muke kwaxayin ya ba mu daga falalarsa, da sun yi hakan, da ya zama alheri gare su, a kan su aibata ka. Yayin da suka aibata Manzon Allah (S.A.W) a wajen rabon sadaka, sai Allah ya bayyana musu inda ake rabata, da waxanda suka cancanta a ba su, don kuvutar da Manzonsa, ya ce:**

**(60) Kaxai zakka ta wajibi ana bayar da ita ga talakawa (Faqirai) su ne mabuqata waxanda suke da dukiya daga wata sana’a ko aiki, amma bata isar su, ba kuma wanda ya kula da su. Ana ba wa miskinai, waxanda kusan basu da komai, kuma halin da suke ciki bai vuya ga mutane ba, saboda yanayinsu ko maganarsu. Ana ba wa masu karvo ta, waxanda shugaba yake aikawa don tara ta. Ana ba wa kafirai waxanda ake jawo hankulansu da ita, don su musulunta, ko kuma masu raunin imani, don imaninsu ya qara qarfi, ko a ba wa wanda za a kare sharrinsa. Ana ba wa bayi, don su samu yanci da ita. Ana ba wa waxanda ake bi bashi, ba tare da varna ko savo ba, in basu samu abin da za su biya bashinsu da shi ba. Ana bayar da ita wajen shirya masu jihadi a kan tafarkin Allah. Ana ba wa matafiyi wanda guzurinsa ya yanke. Taqaita bayar da zakka ga waxannan, farilla ce daga Allah, Allah masanin abin da zai gyara bayinsa ne, mai hikima ne cikin tsarinsa da shari’arsa.**

**(61) Daga cikin munafukai akwai masu cutar Manzon Allah (S.A.W) da magana, suna cewa - yayin da suka ga haqurinsa -: “Ai shi yana sauraren kowa, kuma ya gasgata shi, ba ya bambance qarya da gaskiya”. To ka ce da su – Ya kai wannan Manzo –: “Haqiqa Manzo ba ya jin komai sai alheri, yana gasgata Allah, yana gasgata abin da muminai na gaskiya suke bada labari, yana jinqan su, kuma aiko shi rahama ce ga wanda ya yi imani da shi. Waxanda suke cutar da shi – da kowace irin cuta – suna da azaba mai ciwo”.**

**Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:** **1 - Dukiyoyi da ‘ya’ya za su iya zama sababin azaba a duniya, kuma zasu iya zama sababin azaba a lahira, don haka bawa ya yi mu’amala da su da abin da Ubangijinsa ya yarda da shi, sai ya samu tsira da su. 2 - Raba zakka yana ga shugabanni, su sanya ta a cikin waxanda aka ambata gwagwardon buqata da yadda ya dace. 3 - Cutar da Manzon Allah a kan abin da ya shafi saqonsa kafirci ne, yana kawo azaba mai tsanani. 4 - Ya dace bawa ya zama mai sauraran alheri, ba sauraran sharri ba, ya saurari abin da a cikinsa akwai gyara da alheri, ya kawar da kai daga jin sharri da varna.**

يَحۡلِفُونَ بِٱللَّهِ لَكُمۡ لِيُرۡضُوكُمۡ وَٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥٓ أَحَقُّ
أَن يُرۡضُوهُ إِن كَانُواْ مُؤۡمِنِينَ ٦٢ أَلَمۡ يَعۡلَمُوٓاْ أَنَّهُۥ مَن
يُحَادِدِ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ فَأَنَّ لَهُۥ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدٗا فِيهَاۚ
ذَٰلِكَ ٱلۡخِزۡيُ ٱلۡعَظِيمُ ٦٣ يَحۡذَرُ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ أَن
تُنَزَّلَ عَلَيۡهِمۡ سُورَةٞ تُنَبِّئُهُم بِمَا فِي قُلُوبِهِمۡۚ قُلِ ٱسۡتَهۡزِءُوٓاْ
إِنَّ ٱللَّهَ مُخۡرِجٞ مَّا تَحۡذَرُونَ ٦٤ وَلَئِن سَأَلۡتَهُمۡ
لَيَقُولُنَّ إِنَّمَا كُنَّا نَخُوضُ وَنَلۡعَبُۚ قُلۡ أَبِٱللَّهِ وَءَايَٰتِهِۦ
وَرَسُولِهِۦ كُنتُمۡ تَسۡتَهۡزِءُونَ ٦٥ لَا تَعۡتَذِرُواْ قَدۡ كَفَرۡتُم
بَعۡدَ إِيمَٰنِكُمۡۚ إِن نَّعۡفُ عَن طَآئِفَةٖ مِّنكُمۡ نُعَذِّبۡ طَآئِفَةَۢ
بِأَنَّهُمۡ كَانُواْ مُجۡرِمِينَ ٦٦ ٱلۡمُنَٰفِقُونَ وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتُ
بَعۡضُهُم مِّنۢ بَعۡضٖۚ يَأۡمُرُونَ بِٱلۡمُنكَرِ وَيَنۡهَوۡنَ
عَنِ ٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَقۡبِضُونَ أَيۡدِيَهُمۡۚ نَسُواْ ٱللَّهَ فَنَسِيَهُمۡۚ
إِنَّ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ هُمُ ٱلۡفَٰسِقُونَ ٦٧ وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡمُنَٰفِقِينَ
وَٱلۡمُنَٰفِقَٰتِ وَٱلۡكُفَّارَ نَارَ جَهَنَّمَ خَٰلِدِينَ فِيهَاۚ هِيَ
حَسۡبُهُمۡۚ وَلَعَنَهُمُ ٱللَّهُۖ وَلَهُمۡ عَذَابٞ مُّقِيمٞ ٦٨



**(62) Munafukai suna muku rantsuwa da Allah – yaku muminai – a kan su basu faxi wani abu da zai cutar da Annabi (S.A.W) ba, don su samu yardarku, amma Allah da Manzonsa su ne suka cancanta a nemi yardarsu, ta hanyar imani da aiki nagari, in dai waxannan sun kasance muminai ne na gaskiya.**

**(63) Yanzu waxannan munafukai basu san suna gaba da Allah da Manzansa ba ne da wannan aiki, kuma duk wanda ya yi gaba da su, zai shiga wutar Jahannama ranar alqiyama, za su dauwama a cikinta har abada, wannan shi ne tsoro da qasqanci mai girma.**

**(64) Munafukai suna jin tsoron Allah ya saukar wa Manzansa wata sura da take bayyana wa muminai abin da suka voye na kafirci. Ka ce da su – Ya wannan Manzo –: "Ku ci gaba – Ku munafukai – da izgilinku da sukanku ga addini, Allah zai fitar da abin da kuke tsoro ta hanyar saukar da sura, ko ba wa manzonsa labarin haka.**

**(65) Ya kai wannan Manzo idan da zaka tambayi munafukai a kan abin da suka faxa na suka da zagin muminai, bayan Allah ya riga ya baka labari, tabbas za su ce: "Ai muna hira ne, muna raha, ba da gaske muke ba". Ka ce da su – Ya kai Manzo – Yanzu da Allah da ayoyinsa da Manzonsa kuke izgili?".**

**(66) Kada ku ba da uzuri, da uzururrukanku na qarya, kun riga kun bayyana kafircinku da izgilinku, bayan da kuna voyewa. In mun yafe wa wasu jama'a daga cikinku, saboda barinsu ga munafunci, da tubansu na gaskiya ga Allah, to zamu azabtar da wasu vangare daga cikinku, saboda zarcewarsu a kan munafunci da rashin tubansu daga gare shi.**

**(67) Munafukai maza da mata, sun haxu a halayen munafunci, sun zama savanin muminai, suna umarni da mummunan aiki, suna hana kyakkyawan ayyuka, suna rowar dukiyoyinsu, basa ciyar da su a kan tafarkin Allah, sun bar Allah, basa biyayya gare shi, sai Allah ya qyale su, bai datar da su ba. Haqiqa munafukai su ne waxanda suka fita daga biyayya ga Allah, da hanyar gaskiya, zuwa ga savonsa da hanyar vata.**

**(68) Alqawarin Allah ga munafukai da kafirai waxanda basu tuba ba, shi ne ya shigar da su wutar Jahannama, suna masu zama a cikinta har abada, ta ishe su uquba, kuma Allah ya kore su daga rahamarsa, sannan suna da azaba mai zarcewa.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Munanan ayyukan munafukai suna da yawa, daga cikinsu akwai rantse-rantsen qarya, da gaba da Allah da Manzonsa, da izgili da Alqur'ani, da Annabi da muminai, da tsoron saukar da sura a Alqur'ani da za ta fallasa sha'aninsu, da bada uzurin su na cewa da gangan suke, kuma wasa suke, alhali hakan tabbatar da zunubi ne, kai ! uzuri ne ma mai muni.**

**2 - Ba a karvar wasa a addini da hukunce-hukuncensa, kuma ana lissafa kutsawa cikin littafin Allah da Manzanninsa da siffofinsa ba tare da ilimi da gaskiya ba, kafirci ne.**

**3 - Munafunci cuta ce mai wahalar magani a cikin xan adam, masu wannan cuta sun yi kama da juna a kowane zamani da lokaci, wajen umarni da mummunan aiki, da hana kyakkyawan aiki, da riqe hannaye da qin ciyarwa a kan tafarkin Allah don yin jihadi, da yin abin da ya wajaba a kansu na gaskiya.**

**4 - Sakamako yana zuwa ne irin aikin da aka yi, wanda ya bar umarnin Allah, ya aikata abubuwan da ya hana, shi ma sai Allah ya qyale shi.**

كَٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُمۡ كَانُوٓاْ أَشَدَّ مِنكُمۡ قُوَّةٗ وَأَكۡثَرَ أَمۡوَٰلٗا
وَأَوۡلَٰدٗا فَٱسۡتَمۡتَعُواْ بِخَلَٰقِهِمۡ فَٱسۡتَمۡتَعۡتُم بِخَلَٰقِكُمۡ
كَمَا ٱسۡتَمۡتَعَ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِكُم بِخَلَٰقِهِمۡ وَخُضۡتُمۡ
كَٱلَّذِي خَاضُوٓاْۚ أُوْلَٰٓئِكَ حَبِطَتۡ أَعۡمَٰلُهُمۡ فِي ٱلدُّنۡيَا
وَٱلۡأٓخِرَةِۖ وَأُوْلَٰٓئِكَ هُمُ ٱلۡخَٰسِرُونَ ٦٩ أَلَمۡ يَأۡتِهِمۡ
نَبَأُ ٱلَّذِينَ مِن قَبۡلِهِمۡ قَوۡمِ نُوحٖ وَعَادٖ وَثَمُودَ وَقَوۡمِ
إِبۡرَٰهِيمَ وَأَصۡحَٰبِ مَدۡيَنَ وَٱلۡمُؤۡتَفِكَٰتِۚ أَتَتۡهُمۡ رُسُلُهُم
بِٱلۡبَيِّنَٰتِۖ فَمَا كَانَ ٱللَّهُ لِيَظۡلِمَهُمۡ وَلَٰكِن كَانُوٓاْ
أَنفُسَهُمۡ يَظۡلِمُونَ ٧٠ وَٱلۡمُؤۡمِنُونَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتُ بَعۡضُهُمۡ
أَوۡلِيَآءُ بَعۡضٖۚ يَأۡمُرُونَ بِٱلۡمَعۡرُوفِ وَيَنۡهَوۡنَ عَنِ ٱلۡمُنكَرِ
وَيُقِيمُونَ ٱلصَّلَوٰةَ وَيُؤۡتُونَ ٱلزَّكَوٰةَ وَيُطِيعُونَ ٱللَّهَ
وَرَسُولَهُۥٓۚ أُوْلَٰٓئِكَ سَيَرۡحَمُهُمُ ٱللَّهُۗ إِنَّ ٱللَّهَ عَزِيزٌ حَكِيمٞ ٧١
وَعَدَ ٱللَّهُ ٱلۡمُؤۡمِنِينَ وَٱلۡمُؤۡمِنَٰتِ جَنَّٰتٖ تَجۡرِي مِن تَحۡتِهَا
ٱلۡأَنۡهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا وَمَسَٰكِنَ طَيِّبَةٗ فِي جَنَّٰتِ عَدۡنٖۚ
وَرِضۡوَٰنٞ مِّنَ ٱللَّهِ أَكۡبَرُۚ ذَٰلِكَ هُوَ ٱلۡفَوۡزُ ٱلۡعَظِيمُ ٧٢



**(69) Ku taron munafukai a wajen kafirci da izgili da addini kun zama kamar maqaryatan al'ummun da suka gabata kafin ku, sun fiku qarfi da yawan dukiya da 'ya'ya, sai suka ji daxi da rabon da aka rubuta musu na kayan daxin duniya da sha'awarta, ku ma – munafukai – kuka ji daxi da rabon da aka qaddara muku daga cikin hakan, kamar yadda maqaryatan al'ummun da suka gabata suka ji daxi da rabonsu, kuka kutsa cikin qaryata gaskiya da sukan Manzo kamar yadda suka kutsa cikin qaryata gaskiya da sukan Manzanninsu. Waxancan da suke da waxannan siffofi munana su ne waxanda ayyukansu suka lalace a wurin Allah, saboda kafircinsu, kuma su ne hasarrarru, waxanda suka yi hasarar kawunansu ta hanyar kai su ga halaka.**

**(70) Ashe labarin abin da maqaryatan al'ummu suka aikata, bai zo wa waxannan munafukai ba, da labarin abin da a ka aikata musu na azaba ba, mutanen Annabi Nuhu, da Mutanen Annabi Hudu, da mutanen Annabi Salihu, da mutanen Annabi Ibrahim, da ma'abota Madyana, da garuruwan mutanen Annabi Luux. Manzanninsu sun zo musu da hujjoji bayyanannu da dalilai a fili. Allah bai zalunce su ba, Manzanninsa sun yi musu gargaxi, sai dai sun zalunci kawunansu, saboda abin da suke kai na kafirce wa Allah da qaryata Manzanninsa.**

**(71) Muminai maza da muminai mata, sashensu mataimaka sashe ne, saboda imani ya haxa su, suna umarni da kyakkyawan aiki, shi ne dukkan abin da Allah Maxaukakin Sarki yake so, na dukkan abubuwan biyayya, kamar kaxaita Allah da sallah, suna hana munanan ayyuka, shi ne dukkan abin da Allah baya so, na savo, kamar kafirci da riya, suna yin sallah cikakkiya, kamar yadda take, suna biyayya ga Allah, suna biyayya ga Manzonsa. Masu waxannan siffofin kyawawa Allah zai shigar da su cikin rahamarsa, haqiqa Allah Mabuwayi ne, babu wanda yake rinjayarsa, mai hikima ne cikin tsarinsa da shari'arsa.**

**(72) Allah ya yi alqawari ga maza da matan da suka yi imani da Allah, zai shigar da su Aljanatai ranar alqiyama, waxanda qoramu suke gudana a qarqashin gine-ginensu, za su zauna a ciki har abada, basa mutuwa a cikinta, kuma ni'imar bata yankewa, ya yi musu alqawarin ya shigar da su wasu gidaje kyawawa a cikin Ajannatai na zama. Yarda da Allah zai yi da su, ta fi dukkan wannan abubuwan girma gaba xaya. Wannan sakamako da aka ambata shi ne babban rabo, da ba rabon da ya kai shi.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Sababin da yake sa wa a yi wa munafukai da kafirai azaba iri xaya ne, a kowane zamani, shi ne zavar duniya a kan lahira, da jin daxi da ita, da qaryata Annabawa da makirci da yaudararsu.**

**2 - Halakar da al'ummu da mutanen da suka wuce saboda kafircinsu ne da qaryatawarsu ga Annabawa, kuma a cikin hakan akwai izina ga wanda zai gane daga masu hankali.**

**3 - Masu imani maza da mata al'umma ce guda xaya, maxaurinsu xaya, masu taimakon juna ne, a zukatansu a haxe suke, a cikin soyayya da qauna da tausayi.**

**4 - Yardar Ubangijin qassai da sammai ta fi ni'imar Aljanna girma, saboda nutsuwar zuciya ta fi nutsuwar jiki.**

يَٰٓأَيُّهَا ٱلنَّبِيُّ جَٰهِدِ ٱلْكُفَّارَ وَٱلْمُنَٰفِقِينَ وَٱغْلُظْ عَلَيْهِمْۚ
وَمَأْوَىٰهُمْ جَهَنَّمُۖ وَبِئْسَ ٱلْمَصِيرُ ٧٣ يَحْلِفُونَ بِٱللَّهِ مَا قَالُوا۟
وَلَقَدْ قَالُوا۟ كَلِمَةَ ٱلْكُفْرِ وَكَفَرُوا۟ بَعْدَ إِسْلَٰمِهِمْ وَهَمُّوا۟
بِمَا لَمْ يَنَالُوا۟ۚ وَمَا نَقَمُوٓا۟ إِلَّآ أَنْ أَغْنَىٰهُمُ ٱللَّهُ وَرَسُولُهُۥ
مِن فَضْلِهِۦۚ فَإِن يَتُوبُوا۟ يَكُ خَيْرًا لَّهُمْۖ وَإِن يَتَوَلَّوْا۟ يُعَذِّبْهُمُ
ٱللَّهُ عَذَابًا أَلِيمًا فِى ٱلدُّنْيَا وَٱلْءَاخِرَةِۚ وَمَا لَهُمْ فِى ٱلْأَرْضِ
مِن وَلِىٍّ وَلَا نَصِيرٍ ٧٤ ۞ وَمِنْهُم مَّنْ عَٰهَدَ ٱللَّهَ لَئِنْ ءَاتَىٰنَا
مِن فَضْلِهِۦ لَنَصَّدَّقَنَّ وَلَنَكُونَنَّ مِنَ ٱلصَّٰلِحِينَ
٧٥ فَلَمَّآ ءَاتَىٰهُم مِّن فَضْلِهِۦ بَخِلُوا۟ بِهِۦ وَتَوَلَّوا۟ وَّهُم
مُّعْرِضُونَ ٧٦ فَأَعْقَبَهُمْ نِفَاقًا فِى قُلُوبِهِمْ إِلَىٰ يَوْمِ يَلْقَوْنَهُۥ
بِمَآ أَخْلَفُوا۟ ٱللَّهَ مَا وَعَدُوهُ وَبِمَا كَانُوا۟ يَكْذِبُونَ ٧٧
أَلَمْ يَعْلَمُوٓا۟ أَنَّ ٱللَّهَ يَعْلَمُ سِرَّهُمْ وَنَجْوَىٰهُمْ وَأَنَّ ٱللَّهَ
عَلَّٰمُ ٱلْغُيُوبِ ٧٨ ٱلَّذِينَ يَلْمِزُونَ ٱلْمُطَّوِّعِينَ مِنَ
ٱلْمُؤْمِنِينَ فِى ٱلصَّدَقَٰتِ وَٱلَّذِينَ لَا يَجِدُونَ إِلَّا جُهْدَهُمْ
فَيَسْخَرُونَ مِنْهُمْۙ سَخِرَ ٱللَّهُ مِنْهُمْ وَلَهُمْ عَذَابٌ أَلِيمٌ ٧٩

ثلاثة أرباع الحزب ٢٠



**(73) Ya kai wannan manzo ka yi jihadi a kan kafirai, ta hanyar yaqarsu da takobi, ka yi jihadi a kan munafukai da harshe da hujja, ka tsanantawa duka vangarori biyun, sun cancanci hakan, Jahannama ce wurin zamansu ranar alqiyama, tir da makomarsu.**

**(74) Munafukai suna rantsuwa da Allah a kan qarya, suna cewa: Basu faxi abin da Allah ya faxa maka na zaginka da aibata addininka ba. Tabbas sun faxi abin da aka isar maka akan su, daga abin da yake kafirta su, sun bayyana kafirci bayan da sun bayyana imani, kuma tabbas sun yi niyyar abin da basu samu nasara a kansa ba, na afkawa Annabi (S.A.W). Ba su yi musun komai ba, sai abin da ba za a iya musunsa ba, shi ne Allah ya yi musu falala da wadatar da su daga ganimar da ya yi wa Annabi baiwa da ita, idan sun tuba daga munafuncinsu zuwa ga Allah, tubansu zata zama alheri gare su, fiye da su zauna a kan munafuncin, idan kuwa suka juya baya daga tuba zuwa ga Allah, zai azabtar da su azaba mai ciwo, a duniya ta hanyar kisa da kamu, ya azabtar da su azaba mai ciwo da wuta a lahira, basu da wani majivinci da zai jivince su, ya tseratar da su daga azaba, basu da mataimaki da zai kare musu azaba.**

**(75) Daga cikin munafukai akwai wanda ya yi wa Allah alqawari ya ce,: "Idan Allah ya ba mu daga falalarsa, tabbas zamu yi sadaka ga mabuqata, kuma wallahi zamu kasance cikin mutanen qwarai, waxanda ayyukansu suka gyaru".**

**(76) Yayin da Allah (S.W.T) ya basu daga falalarsa, basu cika alqawarin da suka yi wa Allah ba, suna riqe dukiyoyinsu, sun qi yin sadaka da komai, sun bada baya suna masu bijirewa imani.**

**(77) Sai ya sanya qarshensu munafunci ne tabbatacce a zukatansu har zuwa ranar alqiyama, don uquba gare su, a kan savawa Allah alqawari, da kuma qaryatawarsu.**

**(78) Shin munafukai basu san Allah ya san abin da suka voye na makirci da kaidi a wuraren zamansu ba?, kuma haqiqa Allah (S.W.T) masanin gaibu ne, babu abin da yake vuya a gare shi, daga ayyukansu, kuma zai saka musu a kansu.**

**(79) Waxanda suke aibata masu bayar da sadaka ta nafila daga muminai, suna aibata su da bada sadaka kaxan, haka ma waxanda basu samu abin da zasu bayar ba, sai kaxan, shi ne abin da za su iya bayarwa, sai su yi musu izgili da cewa: "Wane amfani sadakarku zata yi?" Allah yana mayar musu da izgilinsu a kansu, sakamakon izgilin da suka yi wa muminai, kuma suna da azaba mai ciwo.**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Wajabcin jihadi a kan kafirai da munafukai, jihadin kafirai ana yin sa da hannu da sauran makaman yaqi. Jihadin munafukai kuwa ana yin sa da hujja da kuma harshe.**

**2 - Munafukai suna cikin mafi sharrin mutane, saboda su mayaudara ne, suna fuskantar kyautatawa da mummunan abu.**

**3 - Cikin ayoyin akwai dalili a kan cewa warware alqawari da sava shi yana haifar da munafunci, don haka wajibi ne a kan musulmi ya kai matuqa wajen nisantarsa.**

**4 - A cikin ayoyin a kwai yabon qarfin jiki da yin aiki, don suna tsayawa a matsayin dukiya, wannan asali ne mai girma wajen gane tushen gamammen arziki, da yabon sha'anin ma'aikaci.**

ٱسْتَغْفِرْ لَهُمْ أَوْ لَا تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ إِن تَسْتَغْفِرْ لَهُمْ سَبْعِينَ مَرَّةً
فَلَن يَغْفِرَ ٱللَّهُ لَهُمْ ذَٰلِكَ بِأَنَّهُمْ كَفَرُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ
وَٱللَّهُ لَا يَهْدِى ٱلْقَوْمَ ٱلْفَٰسِقِينَ ﴿٨٠﴾ فَرِحَ ٱلْمُخَلَّفُونَ بِمَقْعَدِهِمْ
خِلَٰفَ رَسُولِ ٱللَّهِ وَكَرِهُوٓا۟ أَن يُجَٰهِدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ
فِى سَبِيلِ ٱللَّهِ وَقَالُوا۟ لَا تَنفِرُوا۟ فِى ٱلْحَرِّ قُلْ نَارُ جَهَنَّمَ أَشَدُّ حَرًّا
لَّوْ كَانُوا۟ يَفْقَهُونَ ﴿٨١﴾ فَلْيَضْحَكُوا۟ قَلِيلًا وَلْيَبْكُوا۟ كَثِيرًا جَزَآءًۢ
بِمَا كَانُوا۟ يَكْسِبُونَ ﴿٨٢﴾ فَإِن رَّجَعَكَ ٱللَّهُ إِلَىٰ طَآئِفَةٍ
مِّنْهُمْ فَٱسْتَـْٔذَنُوكَ لِلْخُرُوجِ فَقُل لَّن تَخْرُجُوا۟ مَعِىَ أَبَدًا وَلَن
تُقَٰتِلُوا۟ مَعِىَ عَدُوًّا إِنَّكُمْ رَضِيتُم بِٱلْقُعُودِ أَوَّلَ مَرَّةٍ فَٱقْعُدُوا۟
مَعَ ٱلْخَٰلِفِينَ ﴿٨٣﴾ وَلَا تُصَلِّ عَلَىٰٓ أَحَدٍ مِّنْهُم مَّاتَ أَبَدًا وَلَا تَقُمْ
عَلَىٰ قَبْرِهِۦٓ إِنَّهُمْ كَفَرُوا۟ بِٱللَّهِ وَرَسُولِهِۦ وَمَاتُوا۟ وَهُمْ فَٰسِقُونَ
﴿٨٤﴾ وَلَا تُعْجِبْكَ أَمْوَٰلُهُمْ وَأَوْلَٰدُهُمْ إِنَّمَا يُرِيدُ ٱللَّهُ أَن يُعَذِّبَهُم
بِهَا فِى ٱلدُّنْيَا وَتَزْهَقَ أَنفُسُهُمْ وَهُمْ كَٰفِرُونَ ﴿٨٥﴾ وَإِذَآ
أُنزِلَتْ سُورَةٌ أَنْ ءَامِنُوا۟ بِٱللَّهِ وَجَٰهِدُوا۟ مَعَ رَسُولِهِ ٱسْتَـْٔذَنَكَ
أُو۟لُوا۟ ٱلطَّوْلِ مِنْهُمْ وَقَالُوا۟ ذَرْنَا نَكُن مَّعَ ٱلْقَٰعِدِينَ ﴿٨٦﴾



**(80) Ya kai wannan Manzo ka nema musu gafara, ko kar ka nema su, da zaka nema musu ita sau saba'in, to duk da yawanta ba zata kai su zuwa ga gafarar Allah ba, saboda sun kafirce wa Allah da Manzonsa, Allah ba ya datar da waxanda suka fita daga shari'arsa da gangan zuwa ga gaskiya.**

**(81) Waxanda suka qi zuwa yaqin Tabuka sun yi farin ciki da qin zuwa jihadi a kan tafarkin Allah, suna masu sava wa manzon Allah, suka qi su yi jihadi da dukiyoyinsu da rayukansu saboda Allah, kamar yadda muminai suke yin jihadi, suka ce, suna masu kashe gwiwar 'yan uwansu munafukai: "Kada ku fita a cikin zafin rana". Saboda yaqin Tabuka ya kasance a lokacin zafin rana ne. ka ce da su – Ya kai wannan Manzo -: "Wutar Jahannama, wadda take jiran munafukai ta fi tsananin zafi daga wannan zafin da suke gujewa, da sun sani".**

**(82) Waxannan munafukan da suka qi zuwa jihadi su yi dariya kaxan, a rayuwarsu ta duniya mai qarewa, amma kuma za su yi kuka da yawa a rayuwarsu ta lahira mai dauwama, sakamakon abin da suke aikatawa na kafirci da savo da laifuka a duniya.**

**(83) Idan Allah ya dawo da kai – Ya kai wannan Annabi – zuwa ga wasu vangare daga waxannan munafukan, waxanda suka tabbata a kan munafunci, suka nemi izinin fita tare da kai, zuwa wani yaqin daban, to ka ce da su: "Ba zaku fita tare da ni zuwa jihadi a kan tafarkin Allah ba har abada, saboda hakan ya zama uquba gare ku, kuma don kiyaye varna da zata biyo, idan kun kasance tare da ni, kun yarda da zama da qin zuwa yaqin Tabuka, don haka ku zauna tare da waxanda basa zuwa yaqi daga marasa lafiya da mata da yara.**

**(84) Ya kai wannan Manzo kada ka yi sallah ga kowane matacce daga cikin munafukai har abada, kada ka tsaya a kan qabarinsa don yi masa addu'a da neman gafara, saboda sun kafirce wa Allah da Manzonsa, sun mutu suna masu fita daga xa'ar Allah, duk kuwa wanda yake a haka, ba za a yi masa sallah ba, baza a yi masa addu'a ba.**

**(85) Ya kai wannan Manzo kada dukiyoyin waxannan munafukai ko 'ya'yansu su qayatar da kai, Allah yana nufin ya yi musu azaba ne da su a rayuwar duniya, ta hanyar wahalar da suke sha a kansu, da abin da yake samunsu na masifa, kuma rayukansu su fita daga jikinsu suna kan kafirci.**

**(86) Idan Allah ya saukar da wata sura a kan Annabinsa Muhammad (S.A.W) wadda ta qunshi umarni da imani da Allah da yin jihadi a kan tafarkinsa, sai masu wadata da yalwa su nemi izinin qin zuwa, su ce: "Ka bar mu, mu zauna tare da ma'abota uzuri, irin raunana da marasa lafiya".**

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

**1 - Neman gafara (Wato Istigfari) ko yin wani aiki baya amfanar kafiri, matuqar yana kafiri.**

**2 - Ayoyin suna nuna taqaitaccen tunanin mutum, wanda shi sau da yawa yana kallon hali da abin da yake ciki, baya kallon gaba, da abin da abubuwan da ake ciki zasu haifar.**

**3 - Sakaci da aikin biyayya idan lokacinsa ya yi, yana zama sababin uqubar Allah da dankwafar da bawa daga yin aikin da samun falalarsa.**

**4 - A cikin ayoyin a kwai dalili a kan shar'ancin yin sallah ga muminai idan sun mutu, da ziyarar qaburburansu, da yi musu addu'a bayan mutuwarsu, kamar yadda Annabi (S.A.W) yake yi wa muminai.**

رَضُوا۟ بِأَن يَكُونُوا۟ مَعَ ٱلْخَوَالِفِ وَطُبِعَ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَهُمْ
لَا يَفْقَهُونَ ٨٧ لَٰكِنِ ٱلرَّسُولُ وَٱلَّذِينَ ءَامَنُوا۟ مَعَهُۥ
جَٰهَدُوا۟ بِأَمْوَٰلِهِمْ وَأَنفُسِهِمْ ۚ وَأُو۟لَٰٓئِكَ لَهُمُ ٱلْخَيْرَٰتُ ۖ
وَأُو۟لَٰٓئِكَ هُمُ ٱلْمُفْلِحُونَ ٨٨ أَعَدَّ ٱللَّهُ لَهُمْ جَنَّٰتٍ تَجْرِى
مِن تَحْتِهَا ٱلْأَنْهَٰرُ خَٰلِدِينَ فِيهَا ۚ ذَٰلِكَ ٱلْفَوْزُ ٱلْعَظِيمُ ٨٩
وَجَآءَ ٱلْمُعَذِّرُونَ مِنَ ٱلْأَعْرَابِ لِيُؤْذَنَ لَهُمْ وَقَعَدَ ٱلَّذِينَ
كَذَبُوا۟ ٱللَّهَ وَرَسُولَهُۥ ۚ سَيُصِيبُ ٱلَّذِينَ كَفَرُوا۟ مِنْهُمْ عَذَابٌ
أَلِيمٌ ٩٠ لَّيْسَ عَلَى ٱلضُّعَفَآءِ وَلَا عَلَى ٱلْمَرْضَىٰ وَلَا عَلَى ٱلَّذِينَ
لَا يَجِدُونَ مَا يُنفِقُونَ حَرَجٌ إِذَا نَصَحُوا۟ لِلَّهِ وَرَسُولِهِۦ ۚ
مَا عَلَى ٱلْمُحْسِنِينَ مِن سَبِيلٍ ۚ وَٱللَّهُ غَفُورٌ رَّحِيمٌ ٩١
وَلَا عَلَى ٱلَّذِينَ إِذَا مَآ أَتَوْكَ لِتَحْمِلَهُمْ قُلْتَ لَآ أَجِدُ
مَآ أَحْمِلُكُمْ عَلَيْهِ تَوَلَّوا۟ وَّأَعْيُنُهُمْ تَفِيضُ مِنَ ٱلدَّمْعِ
الجزء ١١ الحزب ٢١ حَزَنًا أَلَّا يَجِدُوا۟ مَا يُنفِقُونَ ٩٢ ۞ إِنَّمَا ٱلسَّبِيلُ عَلَى
ٱلَّذِينَ يَسْتَـْٔذِنُونَكَ وَهُمْ أَغْنِيَآءُ ۚ رَضُوا۟ بِأَن يَكُونُوا۟
مَعَ ٱلْخَوَالِفِ وَطَبَعَ ٱللَّهُ عَلَىٰ قُلُوبِهِمْ فَهُمْ لَا يَعْلَمُونَ ٩٣



(87) Waxannan munafikai sun yarda da qasqanci da wulaqanci ga kawunansu, yayin da suka yarda su zama tare da waxanda suka qi zuwa yaqi, da waxanda suke da uzuri, don haka sai Allah ya rufe zukatansu a dalilin kafircinsu da munafincinsu, saboda haka basa sanin abin da yake da amfani a gare su.

(88) Amma Manzon Allah da muminan da suke tare da shi, ba su qi zuwa jihadi don xaukaka kalmar Allah ba, kamar yadda waxancan suka yi. Haqiqa sun yi jihadi a kan tafarkin Allah da dukiyoyinsu da rayukansu, sai sakamakonsu a wurin Allah ya kasance: samun amfanin duniya kamar cin nasara da samun ganima, da kuma samun amfanin lahira wanda daga cikinsa, akwai shiga Aljanna, da samun rabauta da abin da ake nema, da kuvuta daga abin da ake tsoro.

(89) Allah ya yi musu tanadin Aljannatai waxanda qoramu ke gudana a qarqashin gine-ginensu, za su zauna a cikinsu  har abada, babu gushewa. Wannan kuwa shine babban rabo wanda babu wani rabo da ya kai shi.

(90) Wasu mutane daga cikin qauyawan Madina da kewayenta sun zo suna bayar da uzuri ga Manzon Allah (S.A.W) domin ya yi musu izini su zauna kar su fita jihadi don xaukaka kalmar Allah. Waxansu kuma sun qi zuwa ne ba tare da sun bayar da uzuri na rashin fitar su ba, saboda rashin gasgatawarsu ga Annabi da rashin imaninsu da alqawarin Allah. Da sannu azaba bai raxaxi zata samu waxannan saboda kafircinsu.

(91) Babu laifi ga mata da yara da marasa lafiya da gajiyayyu da makafi da talakawa waxanda basu da abin da za su bayar na dukiya domin shirya kansu, to babu laifi don basu fita zuwa jihadi ba, saboda uzurorinsu, idan sun tsarkake niyya ga Allah da Manzonsa, suka yi aiki da shari'arsa. Babu wata hanyar da azaba za ta afkawa masu kyautatawa a cikin masu irin waxannan uzururruka. Allah mai yawan gafarta zunuban masu kyautatawa ne, mai tsananin jinqai a gare su.

(92) Haka nan babu laifi akan waxanda basu je yaqi ba, waxanda in sun zo wurinka - Ya kai wannan Manzo - suna neman ka ba su dabbar da zasu hau don zuwa yaqin, sai kace da su: "Ba ni da abin hawan da zan xora ku a kai", sai su juya baya, idanuwansu na kwararar da hawaye domin baqin cikin rashin samun abin da zasu xauki nauyin tafiyarsu, daga wurinsu, ko daga wurinka.

(93) Bayan Allah ya bayyana cewa babu wata hanya da za a bi don yin uquba ga masu uzuri, sai ya ambaci waxanda suka cancanci uquba da kamawa da laifi. Sai Ya ce: "Kawai waxanda a ke da damar yi musu uquba da kamasu da laifi su ne, waxanda suke neman izini daga gareka – Ya kai wannan Manzo - na cewa baza su tafi jihadi ba, alhali suna da ikon tafiya, don suna da abin da za su iya kimtsa kansu da shi. Sun yardar ma kawunansu da qasqanci da wulaqanci na zama tare da waxanda aka bari a baya a cikin gidaje, sannan Allah ya rufe zukatansu, basa tasirantuwa da wa'azi. Kuma saboda rufe zukatansu da Allah ya yi, basa sanin abin da zai amfane su don su zave shi, ko abin da zai cuce su don su guje shi.

## Kaxan Daga Abin Da Waxannan Ayoyi Suke Koyarwa:

1 - Masu jihadi zasu samu  dangogin alheri a duniya, in kuma har sun rasa wannan, to suna da babban rabo na Aljanna da kuvuta daga azaba a lahira.

2 - Asali shine: Mai kyautata wa mutane don karamcinsa ba a kama shi da laifi idan an samu wata 'yar tawaya daga gare shi.

3 - Duk wanda ya yi nufin alheri, ya qulla niyya mai qarfi don yin abin da zai iya, amma sai bai samu damar yin abin ba, to ana xaukansa a matsayin wanda ya aikata aikin.